□ □ oh Alhamdulillah! Naji dadi sosai, Allah ya kuma tsarewa ya kuma bada lapia ingatacciya. Nutsuwa da cikakken hankali muna fatan Allah ya horewa duk masu dauke da irin lalurar da ma marassa lapia na gida dana asibiti baki d □□ ya.□□

□□ llahumma Aamin Baba! Aamin.□□

□□ auwa dama abinda nake son ji kenan, Na saka wasu yan kudade a bankin ka sai ka ciro ka bawa masu lura da can din, Ko sa sake zage damtse.□□

□ □ oh Baba Insha Allah! Umma ma na kokarin yin alkhairi a boye ba tare da masaniyar mu ba, Ban nuna mata an gaya mun ba, Banason ta sani. Wallahi sunce takan aika har ta tashar mota a kakkai su kayan abinci.□□

□□ llah Sarki! Angode mata. Allah ya saka da alkhairi.□□

□□ amin Baba.□□

□□ h! Zaka iya tafiya shikenan.□□

Mikewa Habeebullah yayi ya masa sallama, Har ya kai bakin kofa mahaifin nasu ya kira sunan sa,

□ □ a dan sake tattausar ran dan uwan ka, Kafin warwara komai, Sannan kaje chamber din Oluwa nd toluka kace su baka sakon dana basu. Idan ka Karb □□ ka wuce ka kai nan highcourt masinja ya buga stamp a ajiye. Allah ya bada sa □□.□□

□□ oh Baba Insha Allahu! Zan ndan watsa ruwa sai naje. Nagode! Au! Bara na yiwa Mama Ikhlima sallama □□

Saman ya haye da dan sassarfa yana hada matattakalar benen uku uku.

□□ alamu Alaikum □□

□□ a □□ laykm Salam.. Ah Habeebullah!□□

□□ a □□ m Mama.. Ca nai bara na hawo na rage yawan abincin ciki na. Kinga yadda nayiwa abincinnan mugun ta □□ di kuwa? Har zan fice na tuno.□□ a karasa fada yana shafa cikin sa.

□□h haba dai? Kace beyi dadi ba ka tuttura shi kawai.□□

□□na! Dadin ai har ba □□ magana Mama. Naci sosai seda na zazzagaya parlor sau wajen 3 fa. Barin lemon kwakwar nan da nayi gyatsa se kamshin ta. Allah ya kara budi.□□

□□h ai kuwa naji dadi. Lemon nan kuwa akwai shi a freezer, Zan aiko a kawo maka anjima. Kafin nan ya sake tsumuwa.□□

□□odia nake Mama. Bari naje Baba ya aike ni.□□

□□oh Habeebullah! Sai ka dawo.□□

Yana gaba tana biye dashi a baya suka sauka kasan.

□□huta lapia Baba.□□

Ficewa yai bayan sunyi sallama da mahaifin nasu ya wuce sashen su kan sa tsaye. Sai da yai wanka ya leko wajen Umman su, Ya koma biya sashen Ummy ya gayshe ta. Sannan ya wuce aiken da mahaifin nasa ya masa.

DALAAL

Sannu ahankali cikin yan kwanakin nan shakuwa ce ta shiga tsakanin Adeel da Dalaal sosai, Don da zata hadu da wanda Dr Fabio yace ta nema a nigeria Adeel d □□ nne ya kai ta wajen sa. Cikin ikon Allah duk wasu shirye shirye da cike cike da Dalaal za tayi na license exams dinta (Mdcn)tayi shi, Ranar da aka tanadar musu na zuwa zana jarabawar na kusantowa Dalaal tata fi garin da aka tsara anan zasu yi. Nan taje bayan komai ya gudana suka zana jarabawar da sauran wadanda zasuyi jarabawar. Washegari sakamako yafito. Dalaal ta haye. Nan ta kira Ummy ta sheda mata. Bayan wani lokaci da basu wuce kwanaki 65 ba sukayi induction (signing oath paper) dinsu. Daga nan bayan bayan wasu kwanakin akai posting dinsu a asibitoci da dama, Kowannen su an bashi gurbin asibitin da yake so.

Dalaal na zaune ta ajiye carbin da take ja, Ta shafa adduar da ta yiyyi, Sannan ta danna asibitin koyarwa na malam Aminu kano dake jihar ta kano. Gaba d □□ ya jikin ta har wani tsuma yake sosai, So take kawai ta jita a kusa da Ummy, Duk wasu bincike da zata gudanar akan Uncle Sam tayi, Kuma ta gano amsar alamar tanbayar data sa masa.. knocking kofar da akayi ne yasa ta saurin rufe laptop din dake gabanta,

□□es! Come in....□□

□□azzzinn!□□

□□h manager na mu.. Shigo □□

Shiga Adeel yai bakin sa dauke da sallama ya zauna a gefen gado.

□□a kin cike?□□

□□h!□□

□□na kikasa? Fatan dai lagos kikasa ko?□□

Daria Dalaal tayi. Ta dube shi kafin ta mai da kallon ta gefe.

□□ i bazan iya aiki a garin ku ba, Mutane da cunkuso sunyi yawa.□□

□□ yinbo pepper! Kawai dai kice zaki gudu ki bar mu.□□

□□ i na isa? So ya aiki?□□

□□ lhamdulillah likita bokan turai, Wai meyasa to bayan kin wuce dik matakan nan acan K□□ sar anan kuma kika dawo baya?□□

□□ i kasan kowacce kasa da irin tsarin su, So dole ne na bi matakan kasar nan, Nayi jarabawar da komai ma kafin na cigaba da residency dina.□□

□□ ab lallai kuna shan kwakwa, Allah ya bada sa □□ da nasara.□□

□□ amin Kazn □□

□□ o ya labari?□□

□□ abari!? Wai muga yauwa bari muyi tambayoyin mu.□□

□□ auwa kazn! Dama na dade kina ta jamun aji. Maza maza ask me anything.□□

□□ eyasa kuke kiran Aunty Nani maman ku da suna, No ina nufin da inki...□□

□□ eyasa muke kiran mahaifiyar mu da sunan Aunty ko?□□

□□ h..!□□

□□ okacin da tayi aure da aka kawo ta tare da kanwar ta aka hado su. Yar autar su Aunty Siddiqa, Tayi aure ba dadewa, Toh itace me kiran mahaifiyar tamu da sunan Aunty, Da aka haife ni sena taso ina kiranta da Aunty nima, Shikenan Moh da Hissah ke kiran ta suma da haka.□□

□□ oah! Meyasa sana □□ r uncle business ne, Kai kuma ka zama banker? Baka sha □□ war yin irin abunda yake?□□

□□ ana sha □□ war sana □□ r kasuwanci ko? Toh taka maimai har yau nima bazan ce miki ga kasuwancin da Abban mu keyi ba, Naji dai wasu kance yana sana □□ r harkar safarar mai da siyan kadara ya ajiye, Sana □□ i kala kala dai. Toh a secondary school na kasance ina son commerce, Don shi nayi ma. A university kuma sena karanci bangaren banking and finance. Bayan na gama bautar kasa se Abba ya siyamun job offer na bank na fara aiki.□□

□□ h Masha Allah! Moh da Hissah fa? Tun da nazo banga suna zuwa school ba.□□

□□ oh da yafara a china, Se yata bin abokan banza ya fara drugs. Don har yanzu ina tunanin bai dena ba, Shine Abba ya cire shi. Ita kuma Hissah sai yanzu ta fara online na Noun (National open university of Nigeria). Tare da Moh, Sun maida hankali suna yi ko ba sayi bansani ba.□□

□□ oh ka dinga musu fada mana...!□□

□□ abu dasu.. Dadi ne ya musu yawa. Kowanne daga cikin mu Abba ya ajiye masa kudi a bank da gida da jari, So har fada suke suna jikokin suma ba zasuyi talauci ba.□□

Shiru Dalaal tayi na dan wani lokaci, Adeel duk ya damu ya shiga tambayar ko lapia?

□□ akka damu ba komi..□□

□□ e kikeso na siyo mkki?□□

□□ a komai... Yauwa meyasa farkon zuwa na kuka nuna bakuji dadi dana zoba, Duk da har yanzu kai ne kai welcoming dina banda su Hissah.□□

Sosa keyar sa Adeel yai yana murmushi,

□□ an cika son mutane su zo gidan nan ba, Ba Wai don kyamatar su ba. Kawai bana sakin jiki idan akwai bakon fuska a tattare damu, Kuma ban fahimce ki ba sosai alokacin, Sai daga baya na gano kina da hankali sosai, Da nutsuwa, Abun duniya bai dame ki ba, Kina da kawaici sosai, Kuma kinga ke yar uwace ta jini sosai, Bansan ke first cousin dina bace wallahi, Abba dai yace yar uwar mu zatazo daga waje. Kiyi hak□□ ri idan na miki ba daidai ba a baya.□□

Murmushi Dalaal tayi wanda har sai da fararen hakoran ta suka bayyana. Adeel ya Shafa keyar sa yana sakin tattausan murmushin shima.

□□ aki tambaye ni ko inada budurwa ba?□□

□□ eyasa? I □□ not interested.□□

□□ oo! Ki tambaye ni mana kazin.□□

□□ oh kanada ko babu?□□

□□ abu wallahi, Ke fa?□□

□□ na da..□□

Sauya fuska yayi, Ya mike ya tako gaban ta yana kokarin hada idanu da ita tak □□.

□□ antse da ALLAH?□□

□□ annan wane irin tambaya ce? Je ka ma bacci nakeson yi.□□

□□ o na dena dan Allah kiyi hakuri .□□

□□ a hakura jeka.□□

Bude kofa tayi tana mai daga hannun ta, Ta nuna masa waje. Ficewa yai yana rau-rau da idanu, Ita kuma ta rufe kofar harda murza mukulli....

<<<><>>>>

Babu wanda yasan masha'ar da Hissah keyi da maza daga ita sai su sai kuma Allah da ya halicce mu ya kuma yi hani ga bayyana tsiraici ga wanda ba muharraminka ba, tayi nisan da kira ba zai yi mata ba sai dai kawai a zuba mata ido har zuwa lokacin

da Allah zai yi mata hukunci tun anan duniya. Sai karfe tara ta farka tayi wanka da sallah sannan ta fita zuwa parlor tamkar wata ta Allah da ma'aiki.

□□ unty ina kwana.□�

□□ afiya lau sai yanzu kika tashi?□�

□□'a tun dazu ne kasa fitowa kawai nayi sai yanzu.□�

Kai tsaye ta nufi dining ta hada tea ta zuba abinda take bukata ta dawo parlorn kusa da Auntyn su.

□□ bban ku yana ta jira ki fito ya jiki shiru, yace na gaya miki level cord dinku ya fara yi masa maganar jarabawarku yace gobe zakuje a nuna muku inda zakwi jarabawar ku.□�

Wani farin ciki ya mamaye zuciyar Hissah gobe kenan zasu hadu da Lamido dan ajinsu ne da ya fara nuna mata hanyar tanbadewa. Moh ne ya shigo yasha wani irin aski kamar wani irin wando dik ya yage daga gefe nan ashe gayu ne.

□□ oh wannan shigar kuma ya sunan ta?□�

□□ ta ake ya yi ai Aunty.□ Cewar Hissah tana kai soyayyar doya da taji kwai cikin bakin ta.

□□ annan din?!□ Aunty Nani ta tambaya cikin tabe baki.

□□ h wallahi Aunty.□

□□ askiya bakai kyau ba duk gayun nan, Kaje ka sauya kaya.□

□□ ayu kenan ko Ya Moh?!" Hissah ta kuma fada cikin zugawa.

□□ insan ai ba fita take yi ba shi yasa bata ganin irinsu a jikin gayu, Aunty wannan gayun da kike gani dubunnai da yawa aka kawo mun order dinsu.□

□□ ai kace wata mace Moh?□

□□ aba Aunty, Wallahi nayi kyau □

□□ aza je ka sauya shi kafin ranka ya □□ aci □

Mikewa yai da sauri ya koma dakin sa. Saboda bacin rai bai sake futowa ba. Shi ala dole yayi karshen gayu....

MADRID

Dr. T □ G □□□ Nagode sosai, Allah ya saka da khairan. Shafin yau na ki ne domin jin ddin ki □□□□

*_□ AL-□ IBLA_*□□
Na Safiyya Huguma

*_□□ MABU □ IN ZUCIYA_*□□
Hafsat Rano

*_□□ DALAAL_*□□
Na Miss xoxo

*_□□ UBAYD MALEEK_*□□
Na Mamu gee

*_□□ MAKAUNIYAR □ ADDARA_*□□
Na Bilyn Abdull

Lalai daga ji babu tambaya bana ma ZAFAFAN ku da turirinsu suke tafe. Dan dagani kasan za'a ragargaza cakwakiya, soyayya. Tare da nisha □ i □□□□□□□□□□□□□□□□□□.

Gasu duka akan farashi mai rahusar gaske.

Kamar haka □□□□□□□□

□ aya___300
Biyu____400
Uku_____450
Hu □ u____500
Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki □□□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban ta whatsapp shedan biyanku(evidence of payment/Account name)□□□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU □□□□

□ 0903 □ 234 □ 5899

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
TEAM----ZAFAFA BIYAR □□□□□□□□
10/17/21, 2:10 PM - Aisha Adam: *ANNA SATHAF*

0:11:0

Shigowar sa kenan daga school, Hannun sa ri □□ e da wata yar jaka madededeciya d □□ uke da takaddu. Sanye yake cikin kananun kaya. Ya dora blazer akai kalar wandon jikin sa. Yayi kyau sosai, Kayan sun amshi yanayin jikin sa.

□□ aa! Na dawo.□□

□□ h sannu da zuwa! Yanzu ka shigo?□□

□□ higowa ta kenan na tsaya duba sak □□ n daya shigo mun ta mail.□□

□□ kay! Zauna a kawo maka abinci.□□

□□ aa! Na koshi fa.□□

□□ i baka isa ba, Me kaci?□□

□□ a sha yoghurt.□□

□□ hm lalle fa, To ai ba abinci bane, Ka dai dan sake ci. Tun dazu nake ta tiri tirin shirya maka abinci, Yau rana ta musanman kace zaka gwalane ni? Dama Papan ku yace rabon su ne nace a □□ h wallahi.□□

Ba yadda ya iya haka ya hakura da wucewa dakin sa, Ya koma ya zauna akan kujera.

□□ apa ya dawo?□□

□□ h! Ya dawo ya koma dakko su Bushra. Wai school buses din yau an tafi excursion da su.□□

□□ h okay! Allah dawo dasu lapia.□□

□□ amin! Ka karbo?□□

□□ a karbo gashi.□□

Mika mata yai ta karba tana karantawa, Murmushi fad □□ de akan fuskar ta.

□□ asha Allah! Alhamdulillah! Alhamdulillah! Dakyau Dr.! Allah yakara basira, Ya kawo maka babban aiki Aamin.□□

□□ llahumma Aamin Maa!□□

Sunata hira jefi jefi, Ta tashi ta shiga kitchen ta shiga dakko abinci ta jere akan dinning. Cikin haka sai ga prof. Basheer dasu Basma sun dawo.

□□ aaaaayaaaaaa!!!□□

Da gudu suka □□ addare shi suna dariya, labarin makaranta suka fara bashi, Kowacce tana gaya masa na ajinsu.

□□ u kyaleshi yaci abinci dan Allah, Kuje ma ku cire uniforms d □□ nku, Kuyi wanka. Seku dawo.□□

Tafiya suka yi da sauri, Kowanne yanason ya riga fitowa wajen Hafez.

□□ apa barka da rana.□□

□□ arkan mu! Ya ka karbo?□□

□□ h gashi!□□

□□ h Masha Allah! Excellent!□□

Prof. Basheer ya shiga duba sakamakon yana yabawa hafez.

□□ llah ya sanya alkhairi da albarka.□□

□□ amin Papa.□□

□□ a dai dage ba za kaje convocation din ba?□□

□□ allahi! Shi yasa ma na karba certificate din yau, Hayaniya yayi yawa. Kuma kaga Papa na karba na degree da msc. Ya isa □□

□□ akane, Toh Allah ya temaka.□□

□□ amin Yaa rabbi! Ci abincin Hafez!□□

□□ i nagaya miki rabon mu ne.□□
Cewar Prof. Yana dariya.

□□ ab! Tas ze cinye, Sai idan ya rage kwa ci.□□

Dariya sukayi gaba d □□ ya. Hafez ya debi abincin kadan yana ci. Gaba d □□ ya cikinsa kamar koda yaushe a cunkushe yake, Kawai dai dan kar ya gwale Maa ne shi yasa ya shiga cusa abincin. Dakyar ya cinye wanda ya diba.

□□ ayi dadi sosai! Nagode Maa! Thumbs up!□□

□□ unda be cinye ba bara muzo mu zauna.□□

Papa ya fada yana mai mik □□ wa tsaye. Dinning din yaja kujera ya zauna. Hafez na gefe yana kallon yadda Papa ke faman tsokanar Maa. Shi dai murmushi kawai yake.

□□ aa bari na dan watsa ruwa na sakko.□□

Hayewa yai sama da sauri, Dakin sane dama kawai a saman sai babban parlorn wanda suka mai dashi study, Gefe d □□ ya kuma kayan exercise ne a ciki. Dakin sa ya shige ya fada bandaki, wanka yayo hade da alwala ya sauya kayan jikin sa. Daukar certificate din nasa yayi wanda akai awarding dinsa na doctorate degree ya zura acikin takardun sa. Ya faffesa turaruka sannan ya zura takalma ya koma kasa.

□□ a sakko?□□

□□ h! Maa.□□

Guri ya samu ya zauna, Ya nata koyawa su Basmah assignment da aka basu.

□□ afez tunda ka kammala dama jira nayi ka karasa sai mu fara shiri ko?□□

Papa ya jeho masa tambayar yana nazartar sa. Hafez yai shiru kafin ya juya da littafin Basma a hannun sa yana duban papa.

□□ hirin me fa?□□

□□ hirin komawa Luxembourg, Na gaya maka ai tun kwanaki, Yanzu komai ya kammala dama kai kadai nake jira.□□

Hafez ya sauke ajiyar zuciya yana kallon Maa da taki hada idanu dashi.

□□ aa kikace an bar maganar?□□

□□ abu maganar da aka bari. Bansan meyasa tace maka haka ba, Inaga don kana kwance ba lafiya ne lokacin. Kuma kaga saura sessions biyu ka kammala daga wajen su Dr. Fabio ko?□□

Shiru Hafez yai yama rasa abunda labban sa zasu furta. Yaja kasan leben sa yana ciza.

□□ o bakaji ba?□□

□□ aji Papa! Ban gama shirin da nake ba.□□

□□ ane shiri kake? Dama karatu ne kuma ka k □□ re.□□

□□ apa me zai hana mu koma kasar mu? Ko yanayin yadda ake sauyawa su Basmah schools yayi yawa.□□

□□ a fadamun sau ba adadi, Ina ce maka ba zamu koma ba, Kasan dai dole nan da wasu shekaru mu waiwayi gida, Amman yanzu dai kam a □□ h! Can ma suna da Drs sosae sun kware a fannin lafiya.□□

Hafez ya sake daga idanu ya dubi Maa, Wannan karon idanun su ya hadu . Tambayoyi ne fal a bakin Hafez , Amma ya kasa samun kwarin jikin fad □□ r su. Bakin sa ya matukar yi masa nauyi. Mikewa yai ya fuce ba tare da yace musu komai ba.

Kai tsaye ya wuce wajen Dr. Fabio, Shi kansa Fabio yayi matuk □□ r mamakin ganin Hafez a yanayin daya ganshi,

□□ afez! Lapia dai ko?□□

□□ a lapia ba Dr. ina cikin damuwa.□□

□□ eke tafe da kai?□□

Dr Fabio ya tambaye shi, Cike da son jin damuwar tasa.

Gyara zama Hafez yai shiga bayyanawa Dr. Fabio komai na dangane da abunda ya kawo shi, Dr. Fabio yayi matukar girgiza da abubuwan da Hafez ya sanar masa.

□□ mma meyasa ka bar wannan babbar damuwar a zuciar ka?□□

□□ a rasa samun karfin gwiwar fada ne, Duk tarin shekarin nan sai yanzu.□□

Ajiyar zuciya Dr. Fabio ya sauke yana mai girgiza kansa. Domin kwarai matuk □□ damuwar da Hafez ke adanata a zuciyar sa shekara da shekaru abar a duba ce.

□□ oh! Abunda za kai d □□ ya ne kawai, Ka tunkari Maa din da maganar, Karka wani ji tsoro ko ka kasa bayyana komai, Ka fito ka zayyane mata duk tarin tambayoyin ka, Da abunda zuciar ka ta yanke.□□

□□ oh Dr. Nagode sosai.□□

Hannu hafez ya bawa Dr Fabio su kai sallama, Ya shige mota ya koma gida zuciar sa, Dauke da kwarin gwiwa. Yana shiga ciki ya same su dukka a parlor,

□□ na kaje Hafez? Papan ku ya le □□ a be gano ka ba.□□

□□ aje wajen Dr Fabio ne □□

□□ eya faru ba dai jikin bane ko?□□

Papa ya tambaye shi da kulawa.

□□□□ h magana kawai mu kayi.□□

Ya fadu haka ba tare daya bayyana komai ba.

Sama ya haye, Saboda tsananin yadda kansa ke juya masa, Sai daya samu ya rage cikin sa. Ya sake yo wanka. Aka kira sallah yayi sallah. Tukun sannan ya koma kasan. Maa ce kawai a parlorn tana kallon news.

□□ aa!□□

□□ a □□ m Hafez □□

□□ kwai dinner da zamuyi da colleagues dina, Nace musu bana ra □□ yi, To an rigada anyi booking komai, Wai kowa da partner dinsa. Shine nakeson muje da ke.□□

Kasa boye farin cikin ta tayi, Ta janyo hannun sa ta zaunar dashi a kusa da ita tana murmushi.

□□ a kasa boye farin ciki na... Yaushe ne?□□

□□ ikin satin nan ne □□

□□ oh Allah ya kai mu Hafez! Amma banyi girma da zuwa as partner dinka ba? Tunda naga zasu fison suga budurwa haka ko? Amma suga mahaifiyar ka godai godai.□□

□□ o ba wani girma Maa! Banda wani partner ni. Meye dan naje da ke, Ke fa kika haife ni. Beside nayi shifting lokacin dinner din awa d □□ ya da gama tasu.□□

□□ oh shikenan! Allah ya kai mu, Amman ya kamata dai yanzu ace kanada budurwa Hafez.□□

□□ na da ita ai..□□

□□ aba dai!? Wacece?□□

□□ an sanar miki komai. Ranar dinner din.□□

□□ oh shikenan Hafezullah, Allah ya kai mu.□□

□□ amin Maa!□□

Zama yai, Suka cigaba da kallon labaran da ake nunawa a tashar talabijin din da suke kallo. Jefi jefi sukan taba hira, Duk kuwa da zuciar Hafez a cunkushe take, Bayason nuna mata ne kawai.

****LAGOS****

Zaman kadaicine ya ishi Dalaal, Aunty Nani tun safe suka fita kasuwa da masu aiki. Gashi abokin taya ta hirar baya nan yana wajen aiki. Mikewa tai daga zaman da take ta yafa wani mayafin doguwar rigar ta akan riga da skirt din dake jikin ta. Hanyar parlor ta nufa, Dama kafin ka karasa parlorn seka wuce dakin Hissah.

Gidan shiru ba alamun mutane, Sai nishi dake tashi ta dakin Hissah, Har takai bakin kofar parlor ta juya don ganin ko zazzabi ne ya rufe Hissan gashi babu kowa agidan.

Hannunta tasa ahankali ta tura kofar dakin. Abunda idanunta suka gano mata ne yai matukar tayar mata da hankali. Hissah ce tsirara babu kaya a jikinta. Ta dora wayar ta akan mudubi. Tana video call da wani. Ga hannunta tasa a gabanta. Da sauri Dalaal ta juya tana mai rufe idanunta da tafukan hannayen ta.

Istigfari ta shiga kamowa, Gaba d □□ ya ilahirin jikin ta rawa yake yi. Hankalin ta ya tashi sosai na yanayin data samu Hissah, Duk a zatonta nishin rashin lapia ne sai kuma taga akasin haka.

□□ issah.. Hissah..! Hissah □□

Inaaaa Hissah tayi nisan da kira ba zai sa ta jiyo ba, Sosai ta shagala da aikin masha □□ n da take. Dalaal ta zura hannu ta d □□ uke wayar ta katse. Sai a sannan Hissah hankalin ta ya dawo jikin ta. Da sauri ta mike ta rarumo bedsheet ta rufe jikin ta, Idanunta sun firfito waje. Ta rasa yadda za tayi, Tamkar □□ asa ta tsage ta fada don tsananin tashin hankali.

□□ e..meh..men..□□
Takasa furta komai, Jikinta sai rawa yake. Tasa hannu zata kamo Dalaal, Dalaal ta goce tana hararar ta.

□□ arki soma ta □□ ani kazama.□□

Zubewa Hissah tayi a kasa akan gwiwoyinta tana hawaye shab □□ shabe.

□□ an Allah kiyi hak □□ ri.. Karki fad □□ wa kowa.□□

□□ ayi hak □□ ri? Me kikamun? Ki nemi gafarar mahaliccin ki dai, Kin bani Kunya wallahi, Ashe wayon ki da nuna kina tsoron Allah duk karya kike? Kullum cikin gasamin magana kike a yanayin shigar da nake yi, Ni gashi ba yar iskar shiga nake ko wani abun ba, Amma baki da aiki se yadamun magana, Dazu ma najiyo ki ban tanka ki ba. Lalle kinji kunya, Tir da halin ki Hissah, Allah ya shirya ki yasa ki gane gaskiya.□□

Hissah kuka sosai tashiga yi tana kokarin riko kafar Dalaal.

□□ an Allah kakki fa □□ awa su Yaya.□□

□□ eyasa zan gaya musu? Keda mahallicin ki, Ki nemi gafarar sa. Ki kuma yi kokarin nadamar abunda kike aikatawa. Idan bakisani ba, Wannan jikin naki da kike rabawa maza ta waya, Wallahi yawo yake. Rana d □□ ya Inde ba Allah ya kiyaye ba zaki ga magana ta dawo. Bakisan adadin mutane nawa ne zasu gani ba, Kayya! Ni nama rasa mezance miki, Innalillahi wa □□ nna ilaihir raji □□ n.□□

Da sauri Dalaal ta fice tana goge hawayen takaicin bakin cikin Hissah. Hissah kuwa mikewa tai daga dur □□ ushen datake tai sauri ta maida kayan jikin ta. Gaba d □□ ya jikin ta rawa yake mata. Tunani kawai take Dalaal zata gayawa su Adeel komai. Tana karasa saka kayanta takoma parlor ta zauna tana mai kalle kallen ta inda dalaal Zata bullo.

Ita kuwa Dalaal, Adduar neman shiriya tayiwa Hissah, Ta kade gado tai kwanciyar ta saboda yadda bacci ke daukarta. Daman ka □□ da ne Idan har batada abunyi kuma tagama komai. Takan zube akan gado taita kwasar bacci...

Pls follow, like and refer my small business to your beloved ones □□□□□□□ instagram: yerwaincense_and more.

*_□□ AL-□ IBLA_*□□
Na Safiyya Huguma

*_□□ MABU □ IN ZUCIYA_*□□
Hafsat Rano

*_□□ DALAAL_*□□
Na Miss xoxo

*_□□ UBAYD MALEEK_*□□
Na Mamu gee

*_□□ MAKAUNIYAR □ ADDARA_*□□
Na Bilyn Abdull

Lalai daga ji babu tambaya bana ma ZAFAFAN ku da turirinsu suke tafe. Dan dagani kasan za'a ragargaza cakwakiya, soyayya. Tare da nisha □ i □□□□□□□□□□□□□□□□□.

Gasu duka akan farashi mai rahusar gaske.

Kamar haka □□□□□□□□

□ aya___300
Biyu____400
Uku_____450
Hu □ u____500
Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki □□□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban ta whatsapp shedan biyanku(evidence of payment/Account name)□□□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU □□□□

□ 0903 □ 234 □ 5899

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
TEAM----ZAFAFA BIYAR □□□□□□□□
10/17/21, 2:10 PM - Aisha Adam: _*NH 12*_

ZAFAFA BIYAR NA KUDI NE, DAN GIRMAN ALLAH KI BIYA KI KARANTA □□□□

Gaba d □□ ya Hissah a □□ arare take zaune, Da taji bakon motsi zata fara waige-waige ko Dalaal ce. Mikewa tai a zabure ta nufi dakin Moh. Yana kwance yana busa sigari. Yana ganin ta yai sauri ya cillata ta window yana yamutsa fuska,

□□ a akai?□

□□ hm? Ba komai, Kawai ca nai bara na ga ko kana nan.□

Wani dogon tsaki yaja. Ya mata wani kallo na kin renawa kan ki hankali.

□□ alla meya kawo ki?□

Ficewa tai da sauri bata ce masa komai ba. Ta koma parlor ta cigaba da zama. Ba da □□ ewa su Aunty Nani suka dawo daga kasuwa. Jikin ta na rawa ta sunkuci ledoji tashiga kaiwa kitchen. Aunty Nani dasu safara □□ suka tsaya suna kallon ta da mamaki.

□□ unty, Abba ya dawo?□

□□ acce irin tambaya ce wannan? Ya za □□ i na sani Hissah ni da yanzu na shigo gidan. Baki da lapia ne?□

□□ h! A □□ h!□

□□ h ko A □□ h? Idan baki da lapia gwara ki tashi mu tafi asibiti, Naga kin sauya lokaci d □□ ya.□

□□ a..ba komai.□

Mikewa tayi zata shige ciki, Dalaal ta fito da wayar ta a hannun ta.

□□ h Aunty kun dawo?□

□□ un dawo Dalaal, ashe kina ciki?□

□□ na ciki.□

Garin saurin ta shige ciki ta bige flower vase ya fadi ya fashe.

□□ e Hissah meye haka ne? Saurin me kike Ina zaki je?□

Batai magana ba ta shige ciki har tana sake cin tuntube. Safarau ta dakko tsintsiya ta gyara wajen.

□□ annun ku da zuwa.□

□□ auwa Dalaal.□

Kujerar me cin mutane biyu Dalaal ta zauna tana jiran dawowar Uncle Sam. Shiru shiru bai dawo ba, Haka ta koma daki sai bayan sallar magriba sannan taji alamun horn din motar sa. Tana fita sukai kicib □□s da Adeel za shi wajenta.

□□anager na mu..□□

□□ikita bokan turai..□□

□□a dawo ashe?□□

□□a jimawa, Na tsaya na cika cikina nak tukun sannan.□□

□□h lalle.□□

Jerawa sukai tare suka nufi parlor suna hira. Hissa na can gefe tana raba idanuwa.

□□ncle Sam.□□

□□a □□m daughter. Kin wuni lapia □□

□□lhamdulillah uncle.□□

Zama su kayi dukkanin su suna dan taba hira, Hissah dai sam bata sa musu baki.

□□ai me yake damun Hissah ne? Zo nan autar Abba.□□

□□aya san mata Alhaji? Nayi tambayar nayi, Tace bakomi. Kila ran ne ba dadi yau.□□

Moh da Adeel duk suka shiga tambayar Hissah damuwar ta. Amsar d □□ya taita basu kaman dazu. □□a babu komai □□

Wayar Adeel ce tayi □□ara ya dauka da sauri yana karawa a kunnen sa.

□□ubhan □□llah, anan Nottingham clinics din? Bara zanzo yanzu. Eh! Allah ya bashi lapia.□□

Da sauri ya mike zai fita, Har ya manta mukullin mota ya dawo zai dauka bai wa kowa magana ba.

□□ai menene haka ne, Waye ba lapia?□□

□□auri nake Abba, Fareed ne ba lapia, Yayi accident. Yanzu cousin dinsa ya kira ni yake sanar mun.□□

□□ubhan □□llah! Gwara ka hanzarta kaje.□□

***DA sauri Adeel ya fice, Kai tsaye ya wuce asibitin yana gudu a mota tamkar zai tashi sama. Yana zuwa ya same su a emergency. Lameedo na ganin sa ya taso suka gaysa. Nan yake sanar masa yadda abun ya kasance.

□□ubhan □□llah! Yanzu sai yaushe kenan zamu duba shi?□□

□□ai zuwa anjima can. Wai ko da safe haka suka ce □□

Waje suka fita, Shi da sauran yan uwan su Fareed, Anata jajanta lamarin kowa bakin sa dauke da adduar neman lapiyar su.

Har wajen 10 saura suna zazzaune, Lameedo da wani abokin sa na gefe suna hira, wayar Lameedon na hannun wani abokin su yana ganin hotuna. Wata kara ya saki kamar jiniyar yan kwana kwana.

□□ ai Wai Wai! Wace babyn ce wannan?□□

Ya fada yana mai nunawa Lameedo hotan da yake Kallo. Lameedo ya dan tabe baki yana sakatar hakoran sa.

□ □ ata shedaniyar yarinya ce wallahi, harkar da mukayi da ita ta video ita ta temakamin nayi bacci.□□

□□ ai dan iska. Allah ya shrye ka nawaje na, Amma fa kana kallon ganima wai! Duk itace nan?□□

□□ tace.□□

Adeel dai yana gefe yana sauraron su, Shi haushi ma suke bashi yadda suka dage suna hirar wani abu daban, Baya ma □□ Lameedon da dan uwan sa ke kwance ba lapia.

□□ ai kalli wasu ma? Jakar uba ba daraja sam.□□

□□ abu.. Kwata kwata. Mace da akasan ta da k □□ ma, Kusan dik jikin ta al □□ ura shine wasu jakan suke zubar da tasu. Kuma fa mahaukaciyar gani take zan aureta ko? Kasan Allah aboki, Ko wani dana sani naga zai auri yarinyar nan, Kai ko labari naji zai aureta bansan shiba, Kasan Allah sena aika masa dasu ya fasa aurenta. Shegiya.□□ Lameedo ya karasa fada yana sakin tsaki.

□□ ameedo kaji tsoran Allah □□
Adeel ya fada yana girgiza kai. Saboda tsabar takaicin jin kalaman sa, Duk kuwa da bai san akan wa suke maganar ba.

□□ llah bros! Yarinyar ce ballagaza, Kuka fa take tana kirana a waya. Sai nazo online, Kuma ba akai na kadai ba. Wani babban mutumi dana sani, Yanada mata ma, Har shi suke ire iren abubuwan nan. Ni wani lokacin har tsoro take ban. Yar karama amma tasan manyan abubuwa.□□

Adeel yai murmushi yana dan bubbuga gaban kansa dake sara masa.

□□ uga fuskar ta dan Allah! Saboda nagaji da zancen ta da ake. Ina fatan Allah ya shirya ta.□□

Abokin Lameedo dake gefe ya janyo wayar daidai saitin Adeel yana nuna masa.

□□ yakkyawa kamar ita tayi kanta.□□

Ganin sa da jinsa ne suka tsaya na yan dakikai, Saboda fuskar Hissah daya gani tarwal. Kasa boye damuwar sa yai, Ya danne dakyar yana mai mika wa abokin Lameedo wayar. Shi kuma ya karba ya cigaba da kallon ta yana cewa,

□□ allahi kyakkywa shege aina kuka hadu da ita?□□

□□ school. Noun dinmu, Munyi wani group assignment in person, To anan muka fara sanin juna.□□

□□ ar wacece?□□

□ □ allahi ni ko sunan babanta bansani ba. Bansan yar waye ba. Kasan da iya registration number kawai muke amfani.□□

□□ h eh..□□

Mikewa Adeel yai da sauri, Suka shiga tambayar sa ko lapia? Dakyar ya daure yana dafa goshin sa.

□□ allahi kai nane yaketa ciwo tun dazu..□□

□□ h naga dazu kaman kana bubbuga shi. Sannu Allah ya sawwake.□□

□ □ amin, Yanzu ma gida zan wuce na dawo da safe. Zan tsaya a pharmacy nasai magani sena tafi.□□

□□ o shikenan, Angode. Allah yakara sauki.□□

Wucewa yai, Ya shige mota ya kama hanyar gida, Yana tafe a mota yana hawaye. Gaba d □□ ya hirar su Lameedo ce ke masa yawo a kai, Da hotan fuskar Hissah. Ya nata jan salati yana dukan sitiyari.

DALAAL

Bayan fitar Adeel ba jimawa Dalaal ta shiga d □□ ki tayo sallah ta fito. Sai data bari Alhaji sameer ya gama kallon news tukun ta fara masa zancen daya kawota ta k □□ rk □□ re da,

□□ anyi reporting nan da 2 weeks. Shi yasa nakeson tafiya da wuri saboda zan dan dudduba yanayin asibitin da sauran su.□□

Shiru Alhaji Sameer yai na dan wasu lokuta, Kafin ya dago ya dube ta.

□□ in tabbata ba hadin baki bane da mahaifiyar ki?□□

□□ beg your pardon. Ummy? Uncle sam bangane ba □□

Da alama sub □□ tar baki yayi, Ko kuma tambayar zuciar sa ce ta fito baka. Da sauri ya girgiza kai yana furzar da iskar bakin sa.

□□ a abunda nake nufi ba kenan, Toh Allah ya kai mu, Ba kud □□ awajena yanzu, Me gidan mu da muke harka dashi ya rike kud □□ n, Kinsan nan gidan ma nasa ne ya arana mana.□□

□□ a damuwa Uncle Sam. Inada ragowar wanda aka sallameni a asibitin mu na can □ □

□□ anzu yaushe zaki tafi?□□

□□ obe In Shaa Allah!□□

□□a wuri haka?□□

Ita dai murmushi tai kawai, Ta bud □□ baki zatai magana kenan Adeel ya shigo a razane kamar an hankado shi.

□□na Hissah?□□

□□eya faru? Menene kiran ka tayi? Batada lapia ko?□□

□□ane rashin lapia Abba? Yau sai na karairayata na lakada mata na jaki dan uban uban ta.□□

□□ai meye haka? Me tayi zaka dake ta? Kai dukan ka ake?□□

Adeel yana huci kamar zaki ya tafi d □□kin Hissah, Danko wuyanta yai, Ya shiga ball da ita yana huci. Su Aunty Nani suka firfito ana tambayar sa meya faru? Nan yake sheda musu komai. Kowa jikin sa yai sanyi. Moh ya shiga ba Adeel hakuri yana k □□k □□rin riko hannun sa,

□□akar ni, Shashasha kai ma can daya gaula, Ka girma baka san ka girma ba. Kamar kai ace har yanzu kana shaye shayen da kake yi, Duk kanwar ja ce kai da ita. Kai Allah ya sawwake. Abba kayi gaggawar bada yarinyar nan sadaqa ga wanda zai temaka ya iya aurenta. Shi kuma Moh ka kai shi gidan mari su ladabtar dashi.□□

Uncle sam yaja tsaki yana girgiza kai, Zama yai akan kujera yana dafe habar sa. Adeel sai maimata abun da ya fad □□yake.

□□ai ne zaka gayamun abunda zan yanke ne?□□

□□bba... Dan na fa □□a lefi ne? Ku □□i kake sakar musu da yayi yawa Abba, Moh ya zama cikakken dan kwaya, Hissa kuma ta zama yar kanta, Lokacin da muna cikin halin rashi ai idanun su basu bude har haka ba..□□

□□e kake nufi Adeel?□□

□□lhaji dan Allah kayi hakuri, Kai Adeel bashi hakuri, Idan bacin rai yayi yawa, Ba bude baki ake ai magana barkatai ba. Sai hankula su tashi.□□

Ganin abun na neman wuce gona da iri, Dalaal ta mike da sauri tai dakin ta. Batason tashin hankali, Gaba d □□ya ta rude. Duk da rufe k □□far da tayi tana jiyo hargagiyar su. Batasan sanda suka dena ba, Dan Itama seda dare yaja sosai ta iya yin bacci bayan tayi sallar nafila.

WASHE □□ARI

Da wuri Dalaal ta tashi saboda jirgin da zata bi karfe 12 ne na rana, Don haka tagama kimtsa komai da sassafe ta zura bakar abayar ta. Ranar saboda b □□cin rai ba aci abinci yadda aka saba akan dinning ba, Da alama kowa shi kad □□i aka kai masa. Saboda Dalaal na shirin fita parlorn sai ga safarau takai mata nata.

A tsaitsaye ta dan caccakuna taci, Tana mai duba agogon hannun ta. Saboda ya zamar mata kamar almara duk sanda zatai tafiya se ta makara, Ko tayi missing flight ma gaba ki daya. Tana gama ci ta janyo akwatun ta. Sauran kayan dama already sunyi kano tun dirarta a lagos.

Lekawa tayi bakowa parlor, Tai knocking kofar aunty Nani, Nan take sheda mata Uncle Sam din ya fice tun asubah, Adeel ma ya tafi aiki. Dalaal taso siyi sallama da Adeel, Saboda bata gaya masa yau ne tafiyar ba. Sallama tayiwa Aunty Nani. Da sauran ma □□ ikatan gidan. Taso siyi sallama da Hissah saboda halin rayuwa, Amma gaba d □□ ya Hissan kofar dakin ta a datse take.

Kalu da Gali ne suka tafi da Dalaal airport, Tana sauka a airport ta kira Ummiey a waya. Bayan sun gaysa ta shiga tambayar ta da.

□□ aye zai zo dauka tama kikace? Saboda yanzu zamu shiga jirgi. Ha-what? Okay Habeeb-bullah? Okay! Alright bye.□□

Ta katse kiran tana mai dagawa su Kalu hannu tashige ciki. Ana gama screening suka shiga jirgi, Bayan yan mintina jirgin ya daga daga jihar ikko zuwa ta Dabo.....

****HAFEZ****

Tsarin yana yin shigar sa da abincin kai har ma da yanayin tsaruwar wajen ya bada kala sosai. Sai da sukaci abinci sukayi nak. Sun dan taba hira tukun sannan Hafez ya shiga zayyanewa Haj Ziyadah damuwar dake zuciar sa, Dama ainihin dalilin daya sa sukazo wajen. Ya kark □□ re yana mai zuba gwiwoyin sa akasa. Hawaye daya na bin d □□ ya, itama Haj Ziyadan kuka take sosai har yaso cin k □□ rfin ta.

□□ an Allah Maaa! Kuyi magana da papa ta fahimta, Wallahi idan ban koma ba zan iya samun wata cutar ta daban, Na matsu, idan akwai gaban matsuwa ma nayi Maa. □□

Goge hawayen ta tayi, A hankali shima ta mika masa tissue ya shiga goge nasa. Muryarta na rawa ta kasa jurar kallon sa,

□□ hikenan Hafez, Bazan tauye maka hakkin ka ba, Kayi hakuri ai. Zan kira kuma Yaya na sanar masa. Kayi hak □□ ri Hafez, Kaji?□□

Girgiza kai yayi yana fyace hancin sa. Ya shiga kwantar mata da hankali.

□□ abu komai Maa! Ni ba kumin komai ba.□□

Haka ya cigaba da tausasarta itama tana kwantar masa da nasa hankalin. Sai da kowanne ya samu nutsuwa sannan suka koma gidah. Kai tsaye ta shige dakin Prof. Basheer ta shiga zayyane masa komai. Bai yi mamaki sosai ba, Dama shima ya kusa gano hakan, Don haka babu wani bata lokaci ya kira embassy kan su fara kintsa musu komai na zuwa kasar Nigeria.

Hafez yana shiga d □□ ki ya zube akan gado yana mai da numfashi. Ji yai gaba d □□ ya tamkar an zare masa wani tokarren abu a zuciar sa na shekara da shekaru.... Fata yake Allah ya cika masa burin sa guda biyu jal da yake muradin kwadaituwar mallakar su.....!!!!!

*_□□ AL-□ IBLA_*□□
Na Safiyya Huguma

*_□□ MABU □ IN ZUCIYA_*□□

Hafsat Rano

*_□□ DALAAL_*□□
Na Miss xoxo

*_□□ UBAYD MALEEK_*□□
Na Mamu gee

*_□□ MAKAUNIYAR □ ADDARA_*□□
Na Bilyn Abdull

Lalai daga ji babu tambaya bana ma ZAFAFAN ku da turirinsu suke tafe. Dan dagani kasan za'a ragargaza cakwakiya, soyayya. Tare da nisha □ i □□□□□□□□□□□□□□□□□□.

Gasu duka akan farashi mai rahusar gaske.

Kamar haka □□□□□□□□

□ aya___300
Biyu____400
Uku_____450
Hu □ u____500
Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki □□□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban ta whatsapp shedan biyanku(evidence of payment/Account name)□□□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU □□□□

□ 0903 □ 234 □ 5899

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
TEAM----ZAFAFA BIYAR □□□□□□□□
10/17/21, 2:10 PM - Aisha Adam: _*OUMMAHMAD COLLECTIONS_*

(WE □□ E GOT YOU&YOUR HOME COVERED)

MUNA SAYAR DA KAYAYYAKI MASU KYAU, INGANCI, DA KUMA RAHUSA □□□□ KAYAYYAKIN MU TUNDAGA NAHIYAR KETARE AKE KAWO MANA SU, DAGA RASSA DA DAMA.

KAMAR SU: Kitchen utensils
_Fabrics _
Shoes nd bag
_Phones _
_Veils _
_Children's wears _
Furnitures

_Dubai,china,India,turkey,Malaysia _

_MUNA GARIN: Kano, Unguwar hotoro _

Facebook handle d □□ nmu: Maryam muhd

Lambar tarhon mu: 07014488636

THIRTEEN

_*OUMMAHMAD COLLECTIONS_*

(WE □□ E GOT YOU&YOUR HOME COVERED)

MUNA SAYAR DA KAYAYYAKI MASU KYAU, INGANCI, DA KUMA RAHUSA □□□□ KAYAYYAKIN MU TUNDAGA NAHIYAR KETARE AKE KAWO MANA SU, DAGA RASSA DA DAMA.

KAMAR SU: Kitchen utensils
_Fabrics _
Shoes nd bag
_Phones _
_Veils _
_Children's wears _
Furnitures
_Dubai,china,India,turkey,Malaysia _

_MUNA GARIN: Kano, Unguwar hotoro _

Facebook handle d □□ nmu: Maryam muhd

Lambar tarhon mu: 07014488636

THIRTEEN

MALLAM AMINU KANO AIRPORT

A hankali ta shiga sakkowa daga matattakalar bene, Wata iska ce ta shiga ratsa ta mai dadi. Lumshe idanu tayi ta bude su, Bakin ta dauke da hamdala na zuwa da sukayi lapia. Tana karasa sakkowa ta nufi wajen kayan ta ta dauka tayi gaba, Hannun ta na dama dauke da wayar ta. Tana cire flight mode din data saka.

Tana cirewa kira ya shigo. Wani masinja dake aiki a wajen ya taho wajen yana ko □□ arin karbar akwatun hannun ta. Kafin ta mika masa akwatun har wayar ta tsinke .

Habeebullah dake tsaye waje ya faka motar sa, ya jingina da bayan motar wayar a kunnensa, Jin ta tsinke bata dauka ba, Ya sake dedeta tsaiwar sa yana duba agogon hannun sa. Tabbas jiya Ummy 12 zuwa da rabi tace jirgin su zai taso. Gashi ya kikkira wayar dalaal din a kashe, Yanzu kuma bata dauka.

Yana tsaye takaici na zafin ranar dake dukan kansa ce tasa shi bude murfin mota ya koma ya zauna yana mai bude murfin ya zura kafafun sa waje. Sanye yake cikin manyan kaya samfurin riga da wando na shadda, rigar irin gajeriyar nan bata kai gwiwa ba, Sai wando. Shud □ □ ya, Ta amsa yanayin jikin sa. Kansa ba hula,

Kanannadadden gashin kansa na fulanin usul ya bayyana. Baki kwantacce kamar na jarirai.

□□ ai me rake.....□

Me raken dake tafe yana tura abun turin da damin raken ke kai ya juyo da sauri yana kalle kallen inda zai hangi me kiran sa.

□□ boki na! Nan zaka yo.□

Da sauri mai raken ya juya yana nufar inda Hafez yake.

□□ a ni yallabai.□

□□ boki na barka da rana..□

Hafez ya k□□ rasa fada yana mai bashi hannu suka gaysa.

□□ annan raken naka na yan gayu ne, Toh a bani nima.□

Mai rake ya dashe baki yana jujjuya raken, Wani ya dakko daga kasa ya shiga sara masa yana kankare shi.

□□ a nawa za□□ baka?□

□□ amun na dari uku aboki na. Ka bani me zaki, Amma fa ba wanda zai sa na manta hanyar gida ba.□

□□ aba ayi haka?□

□□ ab, Kwanaki dana sha wani rake a majalisa can na baro makullin mota ta a zaune nabi aboki na ina rokon ya sauke ni a gidah, Sai da aka janyo ni aka nusar da ni da mota nazo nima.□

Me rake ya rike ciki yana dariya, Hafez ya d□□ uki sala daya yana gabtara suna hira. Sake kiran wayar Dalaal tayi, Yaci sa□□ ta shiga. Ringing biyu ta dauka.

□□ ello...!□

Shiru yai na yan mintina yana sauraren sautin muryar ta...

□□ ello...! Assalamu Alaikum!□
Ta sake cewa tana kalle kallen inda zata hango shi. Wayar a kunnen ta.

□□ aalykm salam, Kina lapia?□

Kallon fuskar wayar tayi kafin ta mayar kunnenta.

□□ hm... Me dauka na ne?□

Hafez dake barzar rake ya sake gyara zaman sa yana sosa gashin girar sa.

□□ h shi ne. Direban ki ba, Amma fa a yau. Yauwa kina magana da Habeeb... Habeebullah! Wanda Ummy ta turo ya dauke ki...□

□□hhh my bad.. I □□ sorry, Na fito ina tsaye.□□

□□kay bara na karaso....□□

Cire wayar yai daga kunnen sa bai katse ba, Ya zaro dari biyar ya mikawa me raken,

□□boki na ga kudin ka, Sauran canji a siyawa iyali gishiri.□□

□□odia nake yallabai, Allah ya saka maka da alkhairi.□□

Karbar ragowar raken nasa yai dake cikin leda ya ajiye akan kujerar tukin sa. Sannan ya rufe motar ya mike da wayar a kunnen sa.

□□na jinki.. Ga ni nan.□□

Dalaal na tsaye ta nata waige waigen ta inda zai bullo . Tunda ya taho ta tsaya tana kallon sa. Shima kallon nata yake yi.

□□ece in black?□□

□□i ce. Okay ni ne me shudin kaya □□

Yana karasowa ta tsaya tana karewa fuskar sa kallo, Ta rasa dalilin da yasa ta kasa dauke idanun ta daga kansa, Musanman daga wajen karan hancin sa zuwa bakin sa, Kai har ma da yar kyakkyawar fuskar sa baki d □□ya. Shi din ma kallon ta yake, Yana mai yaba kyawun ta. Tabbas wannan kallo d □□ya za kai mata kasan ta hada jini da tsatson larabawa. Sam bai dauka haka take ba, Saboda bai tab □□ ganin fuskar ta ba, Ko hotan ta gaba d □□ya. Ya kan dai zauna suyi ta hirar ta da Ummy.

□□oh ko dai ba ita bace yar ummin?□□ Wata zuciar ta gaya masa.

□□aba itace mana... Ai ca tai na dakko Dalaal a airport.□□ Ya furta a fili ba tare da yasani ba.

□□beg your pardon!□□

□□fuwan, Ina zancen zuci ne.□□

Sai a sannan Habeeb ya zare wayar daga kunnen sa ya katse. Sake daga idanu tayi ta kalle shi a karo na biyu, Suna hada idanu ta sauke nata da sauri.

□□na yini..?□□

Agogon sa ya daga ya kalla yana mai langabar da kansa,

□□ahiri yini ne ba safiya ba. Lapia lou Miss.....?□□

□□alaal.□□

□□kay me sunan yan gayu. Muje ko? Ga motar can. Bara na tayaki daukar kayan.□□

Kar □□ar akwatun yai a hannun masinjan yana mai zaro nera dari a aljihun sa ya mika masa. Yana gaba tana biye da shi a baya haka suka karasa wajen motar, Ya zura akwatin a boot. Zata bude murfin motar kenan yai saurin karasawa ya bude mata yana murmushi,

□□adies first...!!!□□

□□hank you!□□

Shigewa tai ta zauna. Ya rufe mata kofar sannan ya koma mazaunin driver ya zauna.

□□a rake..□□

Girgiza kai tayi tana gyara zaman agogon dake wutsiyar hannun ta.

□□askia ne, Ku yan gayu baku iya shan rake a haka, Sai dai a tace ruwan a baku.. Wait kin masan rake kuwa ? Kina ma jin hausa sosai? I doubt so.□□

Murmushi tayi jin kalaman sa. Shima murmushin yai mai sauti yana mai murza key din motar da bismillah,

□□llah! Kinsan ku yan gayun nan plus ke din bama bahaushiya bace, Me ma ake ce muku? Oh yes! half-caste (ruwa biyu).ko?□□

□□eah! mestizo...!□□

□□a □□m?□□

□□□□h nace eh ruwa biyu..□□

□□kay □□ Amman da yaren ku ko?□□

Dariya tai ta girgiza kai alamun a □□h!

□□alle sai mun zauna zaki ban labarin sosai dai.□□

Juya kan motar yai ya dauki hanyar fita daga airport din, Tafiya yake a nutse. Slow music na tashi a hankali. Na □□rar ac nata bada iska mai dad □□, Turarukan jikin su sun had □□ sun bada wani irin exotic scent.

□□in taba zuwa kano kuwa?□□
Yai breaking shirun da suka yi.

Kallon yadda suke tafiya take, Motoci kala kala nata tafiya. Wata yellow bus na gefen su. Kwandasta/Conductor ya zuro kansa yana ihun.

□□wale, Gwale..! Na Gwale ya taho mu wuce.□□

□□a taba... Sosai ma.□□

□□h really?□□

Kad □□ kai tayi alamun Eh! Kafin ta sake cewa,

□□h! Mun taba zama anan din ai, Amma bamu wani da □□e ba.□□

□□kay! Allah sarki. To mu kanawan dabo muna miki barka da zuwa...Kash! □□a fada daga k □□rshe yana dafe kansa.

□□ eya faru?□□

□□ ubutar layi nayi, Ko dayake anan muke zaune, Nima fa half-caste ne..□□

□□ h really! How?□□

Dariya ya sheke da ita yana gyara zaman mudubin gaban motar.

□□ h yes! Saboda usuli na yan katsina ne mu, Wani local govt anace masa sandamu. Maman mu da baban mu duk yan canne. Thou baban mu gaskiya su tun tashin su da komai anan aka haife su, Kuma baban su ne dan can din. Shysa baya ma katsinan ci. Amman maman mu cikakkiyar yar cance. Dukan su fulani ne. Muna zaune a kano cikin hausawa kinga kuwa nima ai half-caste ne ko?□□

Dalaal tayi dariya tana dan kallon yadda ya ha□□ikance yana fada kamar gaske.

□□ r half-caste.□□

□□ a□□ m yar gayu... □□

A haka ya cigaba da tuki, Yana ta zuba mata zance, Dan shi Habeeb akwai magana. Ko ya saba da mutum ko bai saba ba. Haka zai ta zuba kamar rediyo. Sannu a hankali har suka karasa□□do bayero Mall..□□

□□ orry! Bara na karbo abu a cikin shop-rite pls □□

Kada kai tayi alamun□□oh. Ya shiga ciki da sauri, Fresh fruits ya siyo da drinks irin wanda yasan zata iya sha. Ya biya ya koma yanata sauri. Tana zaune a gaban mota tana kallon sa tun da ya fito daga ciki. Ya bude murfin baya ya zura kayan, Sannan ya shiga ya koma mazaunin sa yana haki.

□□ ai.. Da yar tafiya cikin nan wallahi. Sorry na bar ki ke d□□ya.□□

□□ akomi.□□

Tafiya suka cigaba da yi, Ya kunna wakar dan kwairo yana bi.

□□ in san shi?□□

□□□□ h!□□

□□ a manta fa ba irin naku bane.□□

Ita dai Dalaal bata kula shi ba tayi murmushi kawai, Ta lura shi din irin mutanen nanne wanda bakunan su basa shiru. Ko baka tanka ba sai sunyi magana. Haka suka cigaba da tafiya yana zuba mata zance, Duk dai akan kwaryar garin kano da abunda ta kunsa, Ita dai Dalaal takan amsa shi, Wani lokacin kuma tayi daria. Har suka karasa unguwar su habeeb dake Magaji rumfa□□lu Avenue..□□ Wani titi mai dauke da kibiya da rubutun *ATTORNEY GEN. SAIFUDDEEN IBRAHIM SANDAMU STREET* Suka shiga. Dalaal tabi layin da kallo me kyau dashi gashi tsit ba kwaramniya.

□□ ar gayu... Mun zo gida.□□

Masu gadi suka bude masa gate ya danna kan motar ciki. Har wajen shiga bangaren Ummy ya kai motar ya faka.

□□ un zo.□□

Fitowa tai tana kallen kowane b □□ ngare. Akwatun ta ya d □□ kko daga boot ya janyo hannun sa yana ja.

□□ ara na dauka.□□

□□ ar shi gayu-gayu, Ai yan gayu basa daukar abu.□□

□□ hank you!□□

□□ nytime..!□□

Har cikin bangaren Ummy ya shige da akwatun Dalaal na biye dashi a baya.

□□ ssalamu Alaikum! Dan kira Ummy a sama kanwata.□□

Cewar Habeebullah ya gayawa mai aikin Ummy dake saka turaren wuta. Parlorn gaba d □□ ya ya gauraye da kamshin sandaliyya.! Zama su kayi akan kujeru. Wayar Dalaal ta fara □□ ara, Dakkota tayi tana dubawa. Kamar yadda ta tsammata shi dinne kuwa. □□ azn □□

□□ ello...□□

□□ aba ya zaki mun haka?□□

Tun kafin ya amsa ta ya fara jeho mata tambaya. Halin Adeel sai shi.

□□ a nayi maka me?□□

□□ ika taho ko ki gayamun? Soo not fair.□□

Ta bude baki zata bashi amsa kenan Ummy ta fara sakkowa daga bene.

□□ orry! I will call u back □□
Kit ta kashe wayar baki d □□ ya.

Da sauri ta mike ta karasa taro Ummy, Suka rungume juna. Dukkanin su fuskokin su sunyi fache fache da hawaye.

□□ mmy! I love and miss you soo much.□□

□□ missed you most hayateey.□□

Habeebullah ya tsaya yana kallon su daga gefe. Hawayen da yake ta ko □□ arin makale masa sai da suka yaudare shi suka zubo. Mama kawai ya tuno, Ya sanya tissue yana gogewa. Mikewa yai yana gyara kasan rigar sa, Duk dan kar su gano yadda idanun sa sukai ja.

□□ mmy bara na dan fita majalisa.□□

Sakin Dalaal tayi, Ta riko hannun ta suka karasa kan kujera suka zauna. Dalaal ta kwantar da kan ta akan kafadar Ummy.

□□ na zaka je daga zuwan ku? Ka zauna kaci abinci gaskia. Na kwada mutumin ka fa. □□

□□ ogale? Godia nake Ummy, Zan dawo to anjima. Idanma ban dawo ba zan aiko a karbar mun. Gayu gayu anzo wajen Ummy an dena kulani kenan.□□

Dalaal tayi dariya, Ummy tai murmushi tana shafa kan Dalaal din.

□□ o shikenan Habeeb, Nagode Allah ya saka da alkhairi ne, Meya faru da idanun ka naga sunyi ja ba dai ciwon kan bane ko?□□

□□ akomi Ummy, Abu ne ya fadamun idon shine na sosa. Bara naje.□□

Ficewa yai da sauri, Can ya dawo ya ajiye ledojin daya siyo fruits a shoprite ya ajiye a bakin kofa.

□□ anwata zo ki shigar musu da shi.□□

Me aikin sanin da ita yake ta taso da sauri ta dakko ledojin ta ajiye agaban Ummy. Ummy ta karbu ledojin tana duddubawa.

□□ h! Angode Allah ya saka da alkhairi, Lalle Habeebullah harda wahala? Har dasu strawberry. Angode.□□

Wayar ta ta dauka zata kira ta mai godiya, Ta gama ringing bai dauka ba.

□□ i nasan bazai dauka ba. Haka yake inde ya maka alkhairi. Allah sarki angode kwarai.□□

Hira suka cigaba da yi da Dalaal ta yaushe gamo? Duk ta cukwikwiye Ummy, Dama ita akwai son jiki, A haka suka ci abinci tare. Sannan Ummy ta rakata dakin da zai zama matsayin nata. Sauran kayan ta da aka karbo a airport tun kwanakin baya Ummyn ta kammalce mata su a gefen closet. Band □□ ki dalaal ta shiga tayo wanka hade da alwala. Already Ummy ta shimfida mata sallaya. Ta zura hijabi ta tada sallah. Sai data idar sannan ta janyo wayar ta ta kunna.

Tana kunnawa sakonnin da Adeel ya tutturo mata suka shigo a jere har uku. Duk akan ta kashe masa saboda me? Sannan kuma akan wane dalili zata taho bata gaya masa ba? Ita dariya ma messages din suka bata. Ta ajiye kenan zata tashi ta sauka wajen Ummy, Kiran sa ya shigo.

□□ ello...manager na mu.□□

□□ abu wani na ku, Bayan guduwa ki kai baki sanar min ba. Meyasa?□□

□□ fuwan, Sanda nake gayawa Uncle Sam baka nan, Kuma ta online nai booking flight, And again zan maka sallama Aunty Nani tace ka fita aiki.□□

□□ uk da haka banji dad □□ ba wallahi. Shigowa na gida kenan dazun zanyi hanyar dakin ki, Aunty ke cemun ai kin tafi. Kinzo sallama bana nan.□□

□□ es! I □□ sorry.□□

□□ azan hakura ba.□□

Dariya tayi kawai tana kokarin cire ribbon din dake daure da gashin ta.

□□ inyi shiru.□□

□□ i ha □□ uri.□□

□□ a □□ i na hakuran. Kiyi mun message kina bani hak □□ ri sannan zan hakura.□□

□□ anda lokaci wallahi.□□
Ta fada cikin gaskiyar ta.

□□ o me zaki mun na hak □□ ra?□□

□□ iddo! Me zanyi kuwa? Ka hakura kawai □□

□□ aye yaron naki? Kiddo ai se ke.□□

□□ a girme ka wallahi.□□

□□ llah ya sawwake, To misali ma kin girmenin meye aciki?□□

□□ othing! Kazn! Bacci nake ji. Sai da safe, A gayshe dasu Uncle Sam.□□

□□ anzun ne zaki bacci ko 9 batayin ba? Kawai dai bakyason ki cigaba da magana da ni ne, Abba kuma baya nan yau gaba d □□ ya ban ganshi a gida ba, Moh yana d □□ ki. Hissa ma na da □□ i maybe, Aunty kuma ta fita biki a ma □□ ota ba dad □□ wa inaga dinner ne.□□

□□ o! Literally, Na gaji ne. Ga bacci inason yi da wuri.□□

□□ kay! Ba matsala.. Kazin. Sai da safe.□□

□□ lright bye! Take kia.□□

Kit ta katse wayar. Ta jona a chaji. Sauka k □□ sa tayi wajen Ummy. Suna zaune ba dadewa Attorney ya kira waya ya dawo zai shigo, Kamar yadda yake ko yaushe. Idan ya dawo daga waje. Seya kira idan kwanan ka ne yaji akwai bak □□ a gidan? Idan akwai baki ya dakata sai sun tafi.

□□ h Alhaji ba kowa, Eh ya dakkota ta. Dazu ba jimawa, To shikenan sai ka shigo.□□

□□ a baban su habeeb nan zaku gaysa.□□

Hijabi ummy ta dakko a gefe ta mik □ □ wa Dalaal ta zura. Ba dadewa Alhaji saifuddeen ya shiga, Gaisawa sukai da Dalaal a mutince har yana tsokanar ta. Daga nan ya wuce parlorn sa dake kasa. Dalaal tayiwa Ummy Sai da safe ta haye sama. Ita kuma Ummy ta nufi wajen Alhaji saifuddeen. An gama shirya masa abinci dama. Tana zuwa ta kara masa sannu da zuwa. Ta zuzzuba masa komai, Yana ci suna hira, Kusan rabin hirar ta Dalaal ce.

MADRID

Yana zaune a wani eatery ya gama cin abinci, Samun kansa yai da janyo wayar sa. Ya danna lambar da ka. Domin ya dade da haddace ta. Yana dannawa sunan da ya rubuta da *TB* ya bayyana. Ringing biyu ya dauka.

Hafez ya sauke ajiyar zuciya yana gyara zaman da yai. Acan daya b □□ ngaren anata magana cikin zakuwa da kwadaituwar jin dadin kiran da akayi.

□□ ello....Hafez! Hafez! Kana ji na?□□

□□ na ji... Ina yini?□□

□□ ai yau harda gaisuwa?Yau girmana ake dakko kenan? Lapia kalau, Ya kake? Ya jikin naka? Ya karatu? Ya komai da komai?□□

□□ omai lapia kalau.. Ya naka?□□

□□ lhamdulillah! Inata cewa Allah yasa ba mafarki nake ba. Idan kuwa mafarki nake, Allah yasa bazan farka daga wannan daddadin bacci ba. Hello kana ji □□

Hafez yai murmushi, Yana mai jujjuya straw din lemonade din gaban sa.

□□ na ji...□□

Hira suka danyi ba mai tsawo ba, Duk kuwa da Hafez ya kasa fadar abunda yasa ya kira. Daga karshe suka yi sallama da juna. Hafez ya mike ya fita ya shige mota ya dau hanyar gida. Yana kan hanya Maa ta kira tana sheda masa cewar angama musu komai na zuwa kasar Nigeria sai dai an samu issue da bangaren su Basma, Visa dinsu ba tayi ba, Wai se ta dau lokaci kan ta fito. Saboda su basu taba ziyartar Nigeria ba. Haihuwar tasu da akai ma a k □□ sar waje akayi..... Bai wani damu ba Shi dai idan zasu koma ko nan da yaushe ne inde ba zasu dau lokaci sosai ba damuwa.

□□ hikenan Maa! Ai ba komai, Inde zasu bayar nan da wani lokaci ai shikenan.□□

□□ h nan da lokaci kalilan suka ce. Inaga ba zefi wata uku zuwa hudu ba.□□

□□ oh Maa! Allah ya kai mu. Sai na dawo.□□

□□ ddah Maimunatu! Gwaggo na bidar ki.□

Labarin da Maimunatu bata karasa bawa Hindu ba kenan. Suka tafi wajen kiran Gwaggo. Hindu ta ciji yatsa. Taso jin karashen labarin.

***. ***. ***

Duk hutu kafin rasuwar iyayen su sai sun ziyarci sandamu sunyi hutu acan. Marigayi Alhaji Ibrahim sandamu shine mahaifin saifuddeen da Ziyadah. Sai mahaifiyar su marigayiya Malama Indo Akilu. Su kadai ne awajen iyayen su su biyu. Daga Alhaji saifuddeen sai hajiya Ziyadah.

A hutun da suke zuwa sandamun ne Alhaji saifuddeen lokacin yana matashi yai tozali da Maimunatu. Kyakkywar bafulatar budurwar data sace zuciyar sa lokaci d □□ ya. Ya kasa nutsuwa. Sai daya samu lokaci ya tsare Maimunatu akan hanya ya gaya mata sakon zuciar sa. Tuni ta bada kai bori ya hau, Domin ita dinma ya burge ta. Domin yanada nutsuwa ga kyawun hali ba kamar matasan karkarar su ba.

Sannu ahankali labarin kaunar da yake mata ta karad □□ dangi da karkarar baki d □□ ya. Soyayya suke gabzawa sosai. Baya kyamatar a kauye take ko rashin zurfin karatu da bata yi ba. Domin iyaka cinta firamare. Kuma dududu alokacin shekarun ta basufi 13 ba, Shi kuma zeyi 20.

A shekarar ne su Hamdiyya da Zaituna kishiyoyin Gwaggo Haule suka kafa kahon zukar sai sun aurar da yaran su. Gashi ko jini basu fara ba. Haka marigayi Malam Aliyu alokacin ya nemi Gwaggo Haule kan ko za □□ hada da Maimunatu? Gwaggo tace a □□ h, Sai ta kara tasawa. Sannan kuma manemin nata karatu yake a birni. Akayi bikin su Ummilo da Haire. A shekarar kowacce ta dawo gida da takardar shika uku. Mazajen sun sausu saboda matsalar yoyon fitsari da suka samu. Sakamakon auren wurin da aka musu basu fara jini ba.

A kwana a tashi ba wuya awajen Allah. saifuddeen ya karasa karatun sa. Aka d □□ ura auren sa da Maimunatu. Lokacin tana da shekaru sha takwas a duniya. Tasha suka da zunde a kauyen saboda ba tayi auren wuri ba. Sa □□ inta kowacce tayi □□ aya da yawa. Ana auren su ba dadewa iyayen saifuddeen suka rasu. Bayan komai ya lafa. Ya dakko matar sa suka dawo kano. Wata tara da aure haihuwa ta taso. A daidai lokacin da tafiyar saifuddeen law school ta tabbata. Haka ya hada yan kudaden sa ya mayar da Maimunatu kauye wajen Gwaggo Haule...

Firgigit Haj Maimunatu ta farka daga baccin da take yi. Ta kasa gane kan mafarkin. Da yanayin data samu Kanta. Data zurfafa da tunani sai kanta ya shiga sara mata. Wata kara ta saki tana dafe kanta. Gwaggo Haule ta tashi da sauri tana tambayarta.

□□ a akai Maimunatu? Minene? Uhm?□□

Babu bakin magana, Sai hawaye da ke kwaranya daga idanun ta. Gwaggo tashiga tofa mata adduoi. Dak □□ ar maimunatun ta cigaba da bacci. Lokaci zuwa lokaci abubuwa da dama kan waiwayo mata kai. Cikin baccin ne tacigaba da tunano ranar da zata haihu. Lokacin suna babban gidan su mai jama □□.....

Tana daga zaune. Cikin ta turtse tse ya taso gaba, Alokacin Gwaggo Haule ta tafi cikin birnin katsina sawo wa Haule kayan aure dan an fara mata tari. Gida ya zama sai kishiyoyin Gwaggo Haule da yara fal. Maimunatu na gefen dakin su. Hadizalo na wanke wanke a bakin rijiya. Yan gidan kuma kowa yana hada-hadar sa. Maimunatu na zaune kan kujerar tsugunno anata labari. Da wannan ya □□ are a saki wancen a dau wani. Anata labartawa kunsan gidan yawa ba □□ rasa guntsi fetsi. Ko baka tanka ba kana tashi za □□ yi da kai. Cikin Maimunatun ya tsufa ainun. Kafafun ta sun kumbura sosai, ita dinma ta kara hawa kamar farashi. Anata hira da ita, Idan ciwon cikin ya motso ta dan cije lebe tayi shiru, Yana lafawa Za □□ cigaba da hira da ita.

Gashi sun je asibiti ance ba haihuwa bace. Ta kara dakatawa. Can ana hira setaga duhu. Du □□um tadena ganin haske. Dake tanada fara □□ sosai. Gashi idanun a bude suke babu wanda zai ce bata gani. Tayi shiru tana jiran sarautar Allah.

□□ama □□na dena gani...□

Mutan gidan suka sa dariya, Kowa ya dauka wasan data saba yi ne.

□□ai Maimunatu, Baki ganin ne idanun ki haka, Kina kallon mu da fara □□?□ Cewar Kubura kishiyar Gwaggo Haule.

Saura suka sa baki. Maimunatu tayi shiru kawai tana girgiza kai.

□□i shikenan tunda baku yadda ba.□

Aka cigaba da hira. Takansa baki. Duk kuwa dai da bata ganin su. Can kamar an kawo wuta. Sai kuma taga tar. Bak □□n ya yaye. Idanun sun dawo nuna mata hotunan komai.

□□a dawo ina gani...□

Sauran suka sa dariya. Kowa na tofa albarkacin bakin sa. Harda masu sharo karyar dama wani lokacin ganin ka kawai seya dauke ya dawo. Nan aka cigaba da hira. Can gari ya lullube da hadari. Kan kace me ruwa ya kece. Kowacce ta shige daki . Hadizalo ta tafi dakin yara suka cigaba da yar carafke. Maimunatu kuma ta koma daki tana ciccije leben ta. Wani azababben ciwon ciki ne ya turniketa. Tashiga salati. Kunsan babban gidan kauye. Tsakanin daki da daki akwai rata/tazara sosai. Ga karar zubar ruwan sama. Shi yasa kowa bai jiyo Maimunatu ba.

Cikin haka Gwaggo Haule ta dawo daga kasuwa tana shiga dakinta dauke da sallama ta hango Maimunatu a sankare. Kafafunta a sama. Idanun ta sun kafe. Tanata wata irin jijjiga. Ai da sauri ta callara ihu, Mutan gidan kowa yazo. Aka fara tambayar meya faru? Domin ba dadewa aka gama zantawa da ita. Har ake gayawa gwaggon duk abunda ya faru. Balan da Gwaggo zata saka ya kira saifuddeen baya nan ya tafi aikin wankin mota acikin gari.

Da sauri ta koma waje ta nemo dan kurkura aka kinkimi Maimunatu aka zura a adaidaita sahun, Suna zuwa asibiti aka rasa gado. Wai sai dai su jira. Gashi tanata jijjiga. Dak □□ar Gwaggo ta zube akasa tana kuka, Likitocin suka kinkimi Maimunatu suka ajiyeta a wani daki na ajiyar kaya. Da sauri suka fara bata duk wani temako daya ce. Gaba d □□ya a galabaice take. Gashi masu haihuwan na da yawa. Ta dau tsawon lokaci tana labour. Dak □□ar aka samu wani likita ya tsaya akanta. Ya fara samata ruwan inducing. Nan ma ba wani cigaba sai ma tagayyara data sake shiga.

Sai ga Bala yazo da sauri, Ashe har ya sanar wa saifuddeen ana sanar masa shima ya dauki hanya ya taho. Suna shirin yi mata aiki a galabai ce ta sunkuto □□an ta kyakkyawa kamar Saiffuddeen yayi kaki ya tofar. Dai dai lokacin da saifuddeen ya iso. Duk su Gwaggo suka furmitsa cikin dakin suna mata sannu.

□□e aka samu....□
Ta tambaya a wahalce tana mai rintse idanun ta saboda yadda wani sabon ciwon kai ya lullube ta.

□□in samu namiji... Maimunatu nahh! Mun samu albarkacin MUHAMMAD-HABEEB-HABEEBULLAH. Allah ya raya mana shi.. Allah ya baki Lapia Maimunatu nah!□

Dak □□ ar ta iya daga kai ta dube su shi da jaririn. Yai masa addu □□ da radin suna alokacin.

***Tana kai wa nan ta farka daga baccin da take, gumi gaba d □□ ya ya sharbe mata jiki.

□□ waggo..! Gwaggo ina Habeebullah?□€

Ta shiga nanatawa tana girgiza kanta.

□□ waggo ina □□ an dana haifa.?□€

Cikin bacci Gwaggo Haule tajiyo muryar Hajia Maimunatu. Ta tashi da sauri tana kara hasken wutar fitilar lagwani. Can sai ga nepa sun kawo wuta wal.

□□ aimunatu! Kin gane ni?□€

Haj Maimunatu ta daga kai tana gyara daurin dankwalin kanta.

□□ a gane ki mana Gwaggo.... Meya faru kike tambaya ta.□€

Gwaggo ta dubi gabas tayi sujjada tana hawaye.

□ □ lhamdulillah Ya Allah kai ne abun godia, Babu komai Maimunatu, Koma kiyi addua ki cigaba da baccin ki, Habeebullah na birnin kano yana karatu. Kin manta kina gida na kinzo duba ni? Koma ki cigaba da kwanciyar ki.□€

Ba tayi musu ba ta koma ta cigaba da baccin ta bayan ta tofe jikin ta da adduoi. Gwaggo kuwa kasa baccin tayi saboda tsabar farin ciki. Ta fita bayi ta yo alwala ta dawo tashiga sallolin godia ga rabbus-samawati wal ardi da fara samun dawowar hankalin Haj Maimunatu. Bayan tarin shekarun da □ □ ka dauka tana fama da matsalar hauka....

**** □⑩€⑩€⑩€□€****

Sannu ahankali duk tarin dukiyar Dalaal dake hannun Alhaji Sameer, Shari □□ h ta kwato mata shi. Gaba d □□ ya ko tsinke dayake a matsayin na mahaifin ta wanda yake na fili dana b □□ ye duk an kwakwushe. Har wanda ya sassayar duk an kwato. Aka bude mata sabon account aka narka mata dukiyar ta aciki. Sauran kadarorin duk aka maida komai da sunan ta.

Za □□ yanke masa hukunci dauri agidan kaso, Ko biyan tarin kudi. Dalaal tace ta yafe. Saboda matsayin sa da yake na mahaifi agareta. Duniya tayiwa Alhaji sameer zafi. Saboda duk ya gama lissafa komai da zaiyi da dukiyar. □□ ar tasan data rage kuma dole ya biya basukan mutane. Masu aikin gidan sa duk ya sallame su. Aunty Nani ma ta kwashe ya nata tayi yaji. Kuma tatafi da Hissa can gidan su zata nema mata mijin aure ko da wanda zai aureta sadaqah idan ta horata ta ladabtu.

Moh kuma Adeel ya kaishi gidan mari. Yace a ladabtar dashi. Shi kuma Adeel din ya nemi tallafin karatu na scholarship zuwa kasar Sweden (country in northern Europe on the eastern part of the Scandinavian Peninsula) Can ya tafi karo karatun matakin degree na biyu a fannin banking and finance. A ranar da zai tafi ya kira Dalaal sun jima suna waya. Ya kuma gaya mata zuciar sa. Matsayin son da yake mata. Kuma

yace ko ta girmeshi bai damu ba. Shi namiji baya kad □□ n. Daya dawo zai aureta inde batai auren ba. Dole a dubi zumunci da kuma muhimmancin Kazn a bashi ita auren sa. Duk sanda ya fadi haka Dalaal kanyi dariya. Kwata kwata ma Adeel baya cikin irin sahun mazan data ke burin aura, Sai dai yanada abubuwa da zata iya duba ta aure shi. Akwai manyan ce, Gayu ga iya kalaman sace zuciyar mace....

MADRID

Yana tsaye jikin calendar yana zagaye date da marker. Can kasan karshen watan kuma ya zagaye shi da kalmar □□-day □□.. Murmushi yai yana jan kasan leben sa. So yake kawai ya ganshi a cikin jirgi zasu koma kasar Nigeria. Rufe marker din yayi da murfin ta ya koma kan kujera ya zauna yana daddanna wayar sa. Cikin haka kira ya shigo da sauri ya dauka yana sanyawa a speaker ganin me kiran nasa *Tb**

□□ ssalamu Alaikum!□□
Hafez ya fada a nutse yana wasa da marker hannun sa.

□□ a □□ laykm salam. Ah □□ h na Morocco sarkin gayu, Hafezullahi hafizin alqur □□ ni. □□

Dariya Hafez yai tamkar ana ganin sa.

□□ odia nake masoyin Allah! Ya gida da komi?□□

□□ apia kalau...! Kai ai fushi nake da kai..□□

Shiru Hafez yai yana mai jinginar da kansa ajikin kujera. Sai da ya sake tambayar sa karo na biyu sannan Hafez ya amsa masa ahankali.

□□ eya...Faru?□□

□□ a fini sani ai, Kai ai halin ka sai kai wallahi, Anyways ya jikin naka?□□

□□ a sauki...□□

□□ aushe zaku taho?□□

□□ oon Insha Allahu..□□
Hafez ya bashi amsa yana mai juya kansa yana kallo calendar din dayai marking da D-day.

□□ anda zaku taho lemme knw..□□

□□ kay □□

□□ eye Labari?□□

□□ ry...□□

□□ o yaushe dai zancen kenan. Kayi budurwar kuwa ko haryan zu bakai ba?□□

□□ ayi, Ban yi ba.□□

□□ angane ba..? Sannu mystery man.□□

□□llah I □□serious, sau d □□ya na ganta. Ban kara ganin taba. So Mysterious (secret of life, life's unexplainable quality)□□

□□angane ba. Bro!□□

□□llah banyi wata budurwa ba. Wadda na gani sau na d □□ya na ganta ban kara ganinta ba. Na kamu da son ta...If it □□ meant to be. It will ba. Idan da rabo, Zan nemo ta□□

□□nsha Allah it shall be well. Kai da ka rike alqur □□ni. Tun kana k □□rami kake hakura da komai sai zab □□n Allah, Insha Allah idan rabon kace zaku sake haduwa. Kai da baka taba soyayyah ba. Rabon kace da yardar Allah □□

□□llah yasa, So ya naka?□□

□□oh gani nan dai, Kasan na taba gaya maka mun rabu da wata first love dina, Tayi aure. So Ummah, Ta kara hadani da wata yar k □□war ta abun bai working ba, Yarinyar idanta ya bude. Amma akwai Wadda nake addu □□r samu yanzu da komai ya dai-daita zan sanar maka.□□

□□kay... Allah ya tabbatar da alkhairi.□□

□□amin □□ na dame ka ko da surutu? Nasan danma ni ne ka iya sakewa kana magana. Shikenan sai na sake kiran ka.□□

□□ill call you back Insha Allah! Thank you soo much. Agayda kowa □□ Hafez ya bashi amsa, Don dagsken ya gaji da wayar. Hannun sa d □□ya nakan kirjin sa saitin wajen zuciar sa.

□□oh Allah ya kara sau □□i, Ka gayda su Aunty.□□

□□a suji Insha Allah.□□

Katse kiran yayi. Ya koma kan gado ya kwanta yana rintse idanun sa. Zuciar sa ce ke masa ciwo sosai, Maganin sa ya dakko da ruwa ya balla ya sha yana sauke numfashi. Don dakyar ya karasa wayar bayaso ya fahimci halin da yake ciki. Yana shanye maganin lokaci kalilan bacci yai awun gaba dashi.

KANO STATE

Attorney ne zaune a bangaren sa, Shi da Habeeb, Dake gefe a kasa yana sauraron mahaifin nasa, Fuskokin su dukka hawaye ne ke tsiyaya kamar ruwan famfo. Attorney ya goge hawayen fuskar sa yana mai cigaba da yi wa Habeeb maganar da suke.

□□aboda haka, Shi Malam Balan daya sanarmun yace mu dakata tukun. Hankalin nata bai gama dawowa duka ba, Da jin haka sai na nemi Dr. Mahmood, Saboda nasan yamin bayani kan cewar da wuya masu irin matsalar (Ad/D) su warke. Sai yake shedamun ana iya dora su kan magunguna da zasu temakawa kwakwalan su. Masuman da ita tata matsalar ba dorarriya bace tasameta ne lokacin haihuwa. Nayi mamakin jin demential state dinta ya dedeta kwarai, Sai Mahmood din ya sake ganar dani cewa, Tabbas shi kansa ya sanarwa dasu Balan cewar lalle karatun alqur

□□ ni da addu □□ in da ake mata ne sukai tasiri agareta. Sauke qur □□ ni kullum da asubah ana rok □ □ n Allah, Kaga kuwa fiye da haka ma zata iya warkewa. Alhamdulillah Yaa rabbi. Dr. Dinma zai zo Yanzu □□

Habeebullah kukan dadi kawai yake yana hamdala. Farin cikin zuciar sa ya ma hanashi magana. Cikin haka Dr. Mahmood ya shigo. Nan suka cigaba da tattaunawa yana sanar musu komai game da ciwon na Haj Maimunatu.

□□ abbas an samu cigaba da cognition enhancing medications, Su ake dora masu irin ciwon ta akai, Saboda sabon psychostimulant modafinil (Provigil) Yana temakawa/improves alertness, a key factor in cognitive performance. ..□□

□□ asha Allahu! Gaskia mungodewa Allah.□□

□□ allahi mai gida, Ni kai na da sauran likitoci munyi mamaki kwarai dagaske , Sai dai kuma dukkan wata cuta da Allah zai dorawa bawan sa, Ya kan warkar da ita a sanda yaso. Ko da kuwa likitocin duniya sun tabbatar ba □□ warkewa. Domin Allah shi buwayi ne gagara misali. Kuma kaga Hajiya Maimunatu ciwukan nata da yawa data hadu dasu wajen haihuwar nan, Ai gaskia jajircacciya cema. Domin badan qur □ □ ni da itadin mai ibada bace ada, Bana tunanin za □□ samu cigaba haka. Duk kuwa da ciwuka ne data had □ □ dasu daga baya. Shiysa dana dudduba gwaje gwajen endoscopy na matsalar cikin da akace tana fama dashi, Dysentry dinnan na colon naga babu shi. Ct scan din kan nata ma naga babu buguwar da muka gani karshe. Jini da sauran gwajen stool duk babu wata matsala. Kuma yanayin yadda naganta jiyan nan da bayanin likitan kwakwalwa yabarmun ganinta na karshe ya shedamun baya tunanin akwai wata sauran hauka a tattare da ita.

□□ uk kuwa da theres no cure for Alzheimer □□/Dementia but there are treatments that may change disease progression, and drug and non-drug options that may help treat symptoms. Understanding available options can help individuals living with the disease and their caregivers to cope with symptoms and improve quality of life.. Kungane ko? So demential state dinta ba wani babba bane duk Kuwa da, Zakaga wani lokacin juna biyu kanzo da matsaloli. Kuma dama Alzheimer □□ disease yanzu kusan a tare suke tafiya inde aka samu irin matsalar ta. Cases na 5 kenan da muka samu bayan nata. Tun wancen shekarun zuwa yanzu, Duk kuwa da gaskiya wancen rasuwa suka yiyyi. Wasu kuma yaran suka samu tabin kai. So shi juna biyu/Pregnancy is associated with improvement in immunoregulation that persists into the geriatric phase. Impaired immunoregulation is implicated in Alzheimer □□ disease (AD) pathogenesis.

□□ o cumulative number of months pregnant, was associated with lower AD risk (□ = □□ 1.90, exp(□) = 0.15, P = .02). Cumulative number of first trimesters was associated with lower AD risk after adjusting for third tri-mesters (□ = □□3.83, exp(□) = 0.02, P < .01), while the latter predictor had no significant effect after adjusting for the former. Wannan duk bayani nake akan sanda komi yasamo asali...□ □

A hanakali ya shiga zayyane musu komai, Habeeb na matse hawayen yadda mahaifiyar tasha wahala. Duk a haihuwar ne tasamu wannan matsalar. Wanda badan Allah ya kawo da baiwar dawowar hankalin taba da shikenan har gaban abadan haka zata zauna in lunacy. Haka Dr. Mahmood dai ya cigaba da musu bayanin komai a takaice tun daga kan, T-cells in AD etiology. T-cells are more numerous in the AD brain than healthy brains...

Sannu a hankali har ya kammala gaya musu komai. Alhaji saifuddeen ya daga hannu sama ya kwararo adduoi yana mai shafawa a fuskar sa.

□□ lhamdulillah! Allah kai ne abun godia.□□

□□ amu cigaba da duba yanayin nata, Kuma na cewa khadija dik yadda ake ciki ta dinga sanarmun. Domin so muke sai komai ya gama dawo mata baki d □□ ya. Sai kuma mu dora ta akan wasu magungunan Insha Allah. Amman dai dan warkewa ta warke. Tasha jinya gaskia. Shekaru kadanne fa a talatin babu, Bazan manta ba. Malamai na ne ke dubata kafin ma na zama consultant nima, Toh dama cikin hukuncin Allah dik abunda yai farko zai yi karshe. Allah ya bata lapia mai dorewa, Ya kuma hadata da ahalin ta da take begen gani baki d □□ ya □□

□□ llahumma Aamin Dr. Allah ya saka maka da alhairi kai ma. Mungode kwarai.□□

Dr. Mahmood bai wani dade ba ya tafi bayan sunyi sallama.

□□ hikenan Habeebullah zaka iya tafiya. Eh mu dan sake bata lokaci, Nan da wani lokaci kalilan sai mu je gaba d □□ ya..□□

□□ oh Baba.! Allah ya kai mu.□□

Habeebullah yai wa mahaifin nasa sallama ya tashi ya fita. Yana fita wayar sa tafara kara. Dalaal ce. Dauka yayi yana saita muryar sa dake alamar yaci kuka.

□□ ello.. Gayu! Okay kina garden. No ina nan. Bara na zo.□□

Dakin sa ya koma ya watsa ruwa saboda fuskar sa tayi alamar kuka. Ya canza kaya zuwa k □□ nana. Ya nufi garden din gidan da Dalaal ke zaman jiran sa. Tun daga nesa suke kallon juna, Amman kowannen su kallon nasa ma □□ nar sa daban. Har ya zauna bata dena kallon sa ba.

□□ otchaaaa! Meye kike kallo na?□□

□□ ake kallo na dai □□

□□ i na dauke idanun ai.. Kece kika cigaba da kallo na.□□

Murmushi tayi kawai tana girgiza kai.

□□ a komai...□□

□□ an yadda ba □□

□□ llah kuwa..□□

□□ o ya whats up?□□

□□ he skyyy □□ tabashi amsa tana daga hannunta sama.

□□ a ki wayon... □□

□□ aga yau kana cikin farin ciki.□□

□□ n sanar mun wani abu ne mafi soyuwa da kusanci a gare ni □□

□□ oah that □□ great! I □□ just bored ne.. Nace bara na kira Esq.□□

□□ a □□ nema na sai kina cikin boredom □□

□□ a wallahi, Kasan kullum ina asibiti ai, Sanda nake free kuma muna tare da kai ai.□□

□□ o ya meye labari?□□

□□ a wani labari, Wai strike ma naji ana tunanin zamu tafi.□□

□□ i ku likitocin nan abu kadan kuce yajin aiki.□□

□□ an kasar ba, Suna wasa da harkar lapia, Amma fault din gwammati gaskia.□□

□□ oh Allah ya kyauta. Kice zaki sha hutu kenan □□

□□ ell.. Not really! Maybe dai naje gidan aunt dina. Tanata damun Ummy.□□

□□□□ na?□□

□□ buja..□□

□□ aba dai yanzu tafiya zaki kibar mu?

□□ iterally yes! Inde strike ya tabbata.□□

□□ oh Allah yasa karya tabbata.□□

Dariya suka shiga yi gaba dayan su. Suka cigaba da hirar su gwanin ban sha □□ wa... Duk wanda ya gansu a yanayin yadda suke sai sun birge shi. Kyawawa dasu duka. Farare. Dalaal ta fishi haske abadan saboda ita ruwa biyu ce. Amman Habeebullah nada wani irin kyawu da kwayar idanu masu tafiya da duk wanda yai tozali da shi. Habeebullah kenan. Barrister dan alkalin alkalai, Babban □□ a yaya ga su Ayaah. Masoyin Allah.!□□□□□

□⑩€□
Littafin DALAAL kirkirarren labari ne, Amma yana dauke da wasu rassa na cikin sa wanda TRUE LIFE STORY NE. Literally! Yes! sun faru, kai suna kan faruwa ma. B □□ ngaren damuwar/depression Hafez ya faru yana kan faruwa ma. Duk kuwa da na canza wasu abubuwan. Sannan bangaren Haj Maimunatu. Wanda abun ya faru dasu. D □□ ya awajen haihuwar tarasu. □□ an ya rayu. D □□ ya kuma bayan ta haihu. Ta samu matslar tabin hankalin a sanadin jijjiga itama. Ta debi shekaru sosai itama da Alzheimer □□/Dementia, Cikin ikon Allah kuma domin shidin mubuwayi ne gagari misali sai ta warke kuma. Akwai case din da ongoing ne yanzu yake faruwa ma, Matar data warke sai haukan ya dawo. Itama duk wajen haihuwa ta samu matsalan. Toh Allah ya bawa bayin sa lapia duk masu dauke da ire iren matsalolin dama marasa lapia na gida dana asibiti baki d □□ ya □□□□□□□□□...

Acigaba da bin alkalamin zafafa don jin yadda labaran su zaku kasance. Yes books din zafafa biyar sun fita daban □□□□

*_□□ AL-□ IBLA_*□□
Na Safiyya Huguma

*_□□ MABU □ IN ZUCIYA_*□□
Hafsat Rano

*_□□ DALAAL_*□□
Na Miss xoxo

*_□□ UBAYD MALEEK_*□□
Na Mamu gee

*_□□ MAKAUNIYAR □ ADDARA_*□□
Na Bilyn Abdull

Lalai daga ji babu tambaya bana ma ZAFAFAN ku da turirinsu suke tafe. Dan dagani kasan za'a ragargaza cakwakiya, soyayya. Tare da nisha □ i □□□□□□□□□□□□□□□□□□.

Gasu duka akan farashi mai rahusar gaske.

Kamar haka □□□□□□□□

□ aya___300
Biyu____400
Uku_____450
Hu □ u____500
Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki □□□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban ta whatsapp shedan biyanku(evidence of payment/Account name)□□□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU □□□□

□ 0903 □ 234 □ 5899

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
TEAM----ZAFAFA BIYAR □□□□□□□□
10/17/21, 2:10 PM - Aisha Adam: *DALAAL*

ZAFAFA2021
(PAID/NOVELS)

KU KAWO TALLAN HAJOJIN KU, ZAFAFA SU TALLATA MUKU, BUSINESSES DINKU SU BUNKASA, AKAN FARASHI MAI RAHUSA

PAGES NA ZAFAFA DA AKEYI YANZU DUKA BOOKS BIYAR NERA 700 NE KACAL!!!

PG: 18

DALAAL

**Tana tsaye gaban mudubin ta irin dogon mudubin nan daka ke iya ganin kanka baki d □□ ya. Sanye take cikin doguwar riga ja ta abaya. Ta yane kanta da mayafin abayar. Bata wani tsaya yin kwalliya ba. Tadai shafa man lebe a bakin ta. Tana mai shafa turare marasa karfi. Wayar ta tadan janyo tayi mirror selfie guda d □□ ya. Ta jefa wayar a jaka ta zuge zip din. Ta sauka kasa tana mai duba agogon dake wutsiyar hannun ta.

A parlorn Ummy ta tarar da baban su habeeb da Ummyn suna karin kumallo. Gaishe su tayi baki d □□ ya tana mikewa tsaye.

□□ mmy zan tafi.□□

□□ aka zaki tafi baki ci abinci ba?□□

□□ asha tea. Ya ishe ni.□□

□□ oh shikenan sai kin dawo. Allah ya kiyaye ya tsare.□□

□□ amin □□

□□ ai kin dawo, Allah ya dawo dake lapia.□□

□□ amin! Baba □□

Sake musu sallama tayi. Ta fita da sauri ganin ta kusa makara.

□□ arinyar nan nada hankali ga nutsuwa □□ Cewar attorney yana mai cigaba da kurbar flavored tea din hannun sa.

Ummy tayi murmushin jin dadin yabon da yake wa Dalaal.

□□ anada manemi ne?□□

Ummy ta girgiza kai, Hade da cewa,

□□ nya kuwa? Nasan dai da tana tare da wani, Amman tacemin sun rabu.□□

□□ ikin yaran nan na keson hadata da wani. Inde batada wanda take so, Allah tana da tarbiyya.□□

□□ oh Alhaji ai kai ubane awajen ta. Allah ya zaba abunda yafi alkhairi.□□

Cigaba da hira suka yi. Har suka kammala cin abincin. Attorney ya mike ya mata sallama ya tafi. Sashen Haj binta ya nufa. Suka gaysa yadan zauna akan kujera yana duban labaran da ake a kujera.

□□ iyasa dai tazama shirme yanzu. Yan siyasa suyita alkawararruka suna rantsuwa akan zasu gudanar da aiyuka, Sai sun hau su juyawa talaka baya.□□

□□ allahi kuwa Alhaji. Kusan haka aketa tafiya dai, Tun shuwagabannin baya da suka rarrasu. Sune dai sukai abin arziki.□□

□□ allahi kuwa, Na yanzu kam kusan duk halin su d □□ ya.□□

Haj Binta tadan yi shiru kafin tace dashi.

□□ lhaji ka kosan Haj Maimunatu tafara samun lapia!□□

□□ h wallahi Hajia! Maganar da nakeson miki ma kenan kika riga ni. Ance kinata aika abin arzuka a boye. Toh angode Allah ya saka da alkhairi.□□

□□ ai Alhaji ni wallahi ba abinda nake nufi ba ma kenan. Toh Allah ya bata lapia mai dorewa. Yasa ta warke kenan baki d □□ ya.□□

□□ oh Aamin ya rabbi. Bari na leka court. Wata sharia zanwa zuwan ba zata. So nake na yanke hukunci a yau. Naga lauyan me kare karar dan shawalwali ne.□□

□□ oh Alhaji, Allah ya dawo da kai lapia.□□

Ficewa yai. Daga nan ya karasa sashen Haj ikhlima itama suka gaisa. Ya wuce wajen aiki.

****

Sannu a hankali wani irin shiri sosai Dalaal suke da Habeeb. Har ta kai ko basa ganin juna su kanyi hirar su a WhatsApp ko ta text message. Habeeb zuciar sa tafara ingiza shi. Wata irin kauna yakewa dalaal acikin zuciar sa da yakasa gane shin wannan so ko shakuwa ce? (Littafi na da bansan wacce duniyar yake ba □□)

Yana zaune akan gado bayan ya bi jam □□ a sallar isha □□ na masallacin gidan su. Chatting suke da dalaal. So yake kawai yai tozali da kyakkyawar fuskar ta.

□□ ina ina?□□

□□ na parlorn Ummy □□

□□ an iya zuwa muyi hira?□□

□□ ure! Why not?□□

□□ mman kunyar Ummy nake....Sede ki fito parlorn baki.□□

□□ hy? Okay fine.□□

Mikewa tai ta janyo hijabin Ummy ta zura. Ummy dake kallon ta tun dazu yadda take murmusawa tana danna waya.

□□ na zaki?□□

□□ ai Habeeb ne zai zo muyi hira. Amma yana kunyan ki. Sede muje parlorn baki.□□

□□ i kuma?□□ Ummy ta fada tana nuna kanta hade da yin dariya.

□□ oh ki gaishe shi. Ki ce na ce ransa ya dade.□□

□□ oh Ummy!□□

Parlorn bakin yana farkon shigowa sashen Ummy daga kasa. Daka bude k □□ fa se shi. Ashe har Habeeb ya rigata zuwa yana zaune. Sanye cikin kananun kaya. Kirar riga da wando. Suna hada idanu taji gaban ta ya amsa.

□□ na yini?□□

Ta fada tana mai zama nesa da shi.

□□ ina lapia?□□

□□ retty Good, Ummy tace tana gaishe ka. Wai ranka ya dade.□□

□□ ubhanAllah me kika gaya mata.□□
Da sauri ya mike ya fita zuwa wajen Ummy.

□□ mmy barka da dare.□□
Ya fada yana sosa keyar sa.

□□ arka Habeebullah. Ai nace bana cin mik □□.□□

□□ aba wane ni...□□

Shiru ne ya biyo baya Ummy ta lura da yadda yafara jin kunyar ta. Yana tsugunne sai faman lankwasa hannaye yake.

□□ oh Nagode Habeeb.□□

□□ oh bara na je. Sai da safe.□□

Mikewa yai ya koma wajen Dalaal. Suka cigaba da hirar su. Can wayar sa tayi kara ya dauka yana kallon sunan me kiran. (TBH)

□□ ello! Na □□ m! Ya kake. Kace ka rike alkawari kenan? Ya jikin naka? Aamin Yaa rabbi. Ai shine fushin da nace ina da kai. Toh Allah ya kawo lokacin. Ya kuma kawo mana ku lapia. Uhm! Zan kira ka... Ya akai ka gane? Toh naji din. Zan kira ka. Zata ji. Alright bye. Take care □□

Ajiye wayar yayi a gefe yana murmushi.

□□ rother na yana gayshe ki.□□

□□ u Na □□ em?□□

□□ o ba su Na □□ em bane. Ban taba gaya miki shak □□ ki na ba? Hamimi? Rabin jiki na da tsoka kenan □□

Dalaal tasa dariya tana girgiza kai.

□□ ab ai kuwa nayi babbar mantuwa. Shi ba anan ya taso ba. Ko a cikin magana ban taba gaya miki na Morocco ba?□□

□□ iterally yes! Kana fadar something Morocco. He □□ nice, attentive, very religious and most caring, Kace cocky being ne amma.□□

□□ abawa sai yazo zaki gani. Zaka mishi tambaya ashirin ya baka amsa d □□ ya. Kayi masa magana sau dari ya furta kalma uku shikenan. Haka halin shi yake. Amma duk duniya idan kika cire fiyayyen halitta da ni kai na, Da iyaye na. Sai shi gaskia.□□

□□ oah... Zuwa zasuyi daga can Moroccan?□□ a tambaye shi.

Habeeb da yana duba wayar sa alokacin ya dan girgiza kai.

□□ o! Daga wata kasar daban. Da dai kam a moroccon suka fara zama. Sunan sa Hafez, Hafezullah. Bari dai sai yazo muna tare zan dakko labarai. Bai taba budurwa ba tun dayake sai akan wata. Kuma har yanzu bai san inda ma take ba.□□

Dalaal tayi dariya tana girgiza kai.

□□ i yafi, Da ace yana kule-kule dinnan.□□

□□ hm da wannan gaskiya. Shi fa baya magana ne. Muma bar zancen sa sai yazo zaki ga komai. Kin ki ban amsar tambayar dana miki. Wane irin namiji kikeso... Kika sani ko miji zan miki.□□

Dalaal ta dan daga kai ta dube shi tana murmushi.

□□ anda yafu alkhairi agare ni.□□

□□ ut still dai kinada taste dole, Kowane dan adam nada buri.□□

Ajiyar zuciya ta sauke.

□□ nason mutum dogo, Mekyau kamar kai haka, Me gayu da iya zance irin na wani cousin dina Adeel. Then mara magana haka wanda kallon mata basu ishe shi ba haka. Kamar misalin brother dinnan naka da kake fada. In general Inason nabi zucia na kawai akan wanda tafiso inde alkhairi ne agare ni.□□

Habeeb ya samu kansa da ka □□ a kai yana murmushi. Can ya taso ya koma kusa da kujerar ta yana zuba mata idanun sa. Data kasa jure kallon nasa.

□□ isali ace nace inason wata mace.... Zata so ni saboda me? Like halina ko wasu abubuwa nawa dai haka? Kinji..... Dalaaal □□

Yadda yaja Dalaal dinne yasa ta zuba masa idanu itama tana kallon sa. Hancin sa da yanayin bakin sa. Kai harda sajen sa da gemu dik irin nasa ne. Kawai dai wancen yafi hasken fata.

□□ ana da kirki... You are nice... way too nice. Literally yes! You are very good natured.□□

□□ odia nake k □□ nwata.. Wata ce zucia ta ta aminta da ita, Ina sonta. Sosai fa! Kuma zan iya auren ta ko da kuwa ayau akace na fito. Koda yanayin hali na da al □□ duna ba su mata ba, Zan iya ragewa zuwa yadda take so, Amman na kasa gaya mata. Tayaya kike ganin zan sanar da ita?□□

□□ awai ka gaya mata.. Ka samu lokaci. Kaje kuyi magana. Ko ka tura mata ta message.□□

□□ an yi kamar yadda kikace, Zan tattaro duk wasu courage na hada waje d □□ ya.□□

Murmushi tayi masa tana sara masa alamar salute. Habeebullah ya mike ya koma inda ya fara zama ya zauna yana murmushin shima. Yadda ya tsareta da idanu ne yasa dalaal ce masa bacci take ji. A dole badan yaso ba. Yai mata sai da safe ya tafi. Zuciar sa na tsara masa yadda zai zayyano mata kalaman kauna ya tura mata. Ko kuma ya ware rana d□□ya su fita unguwa ya gaya mata.....

*******KATSINA STATE*********
(SANDAMU LG)

Kan kace mene? Warakar ciwon tabin kan Haj Maimunatu ya zagaye sandamu da abunda ke cikin ta. Masoya na kusa dana nesa haka suka rika tururuwar zuwa suna musu barka.

□□ddah Maimunatu, Na kai miki ruwan wankan.□□ewar Hadizalo tana mai kallon Haj Maimunatu cike da kulawa.

□□oh Hadiza. Nagode.□□

Mikewa tai sanye da hijabin ta, Ta daura zani a ciki, Bandakin ta shiga. Tayo wanka , Hade da wanke kan ta da shampoo da Hadizalo ta kai. Ta dirje koina a jikin ta sannan ta fito. Mai ta shafa tana mai zura kayan ta.

□□au yaushe Gwaggo?□□

□□araba! Ta bawa ranar samu.□□

□□oh Allah yasa mu samu alkhairi.□□

□□llahumma Aamin.□□

Hira suka cigaba da yi. Mutane nata zuwa suna ganin ta. Ita dai dik wanda ya mata murna amsawa take duk kuwa da bata kamo bakin zaren ba. Haka akaita tudadowa har dare sannan kafa ta dauke.

Haj Maimunatu ta haye kan gado bayan ta yi addu□□in ta ta dauro alwala.

□□waggo wai miyasa mutane keta shigowa duba ni? Nayi rishin lahia ne?□□

□□ahiar ce ta samu Diyar albarka.□□

Bata sake cewa komai ba. Domin takasa gane kan maganar gwaggon. Taja hamma tana mai rufe bakin saboda yadda bacci ke jan ta.

□□waggo sai da safe□□

□□oh Allah ya tashe mu lahia.□□

Juyawa Haj Maimunatu tayi ta lula duniyar bacci. Fanka sai kada su take yi. Sakamakon wutar lantarkin da nepa suka kawo. Gashi anyi ruwa gari yai ni□□ma. Bishiyu sai kad□□wa suke suna bada iska mai dadi.

Cikin baccin da take. Ta cigaba da tunano rayuwar ta ta baya data shud□□. Kamar dai cigaba akan tuna bayan da tayi....

□□ai na da cikina wani irin ciwo suke yi Gwaggo.□□

□□ iyi hak □□ ri d □□ yar albarka, Mai gidan naki yace idan muka koma zai dakko kwararren likita ya sake duba ki, Tunda nan din kinga likitocin sunce ba gado kuma asibiti ya cika. Sunce kin rigada kin haihu lahia me za □□ zauna a musu. Kina ganin tun dazu suke aikowa mu tafi □□

Ciccije lebe kawai take tana dan dafe kasar marar ta. Gwaggo na goye da Habeebullah yanata baccin sa. Hadizalo da su Iya Ramma aminiyar Gwaggo, su suka temakawa Haj Maimunatu ta gyara jikin ta. Aka zura mata hijabi.

Saifuddeen ya dakko shatar mota ta debo su suka koma gida. Yana ta mata sannu. Ita dai dauriya kawai take. Da dare jiki ya kara tsananta. A dole aka kara daukar ta suka nufi babban asibitin cikin birni. Duk likitocin basa nan. Sai nurses su kuma sunata yanga. Suka dura mata ruwa suka bata gado. Ciwo nata cinta tana salati. Haka ta kwana d □□ ya tana sallallamin sabon ciwo. Likitocin basu zo kanta ba ganin ai ta haihu wai zazzabi ne kawai. Sai da sukaita roko tukun sannan wani babban likita yazo washegari. Yana dubata yace ai wata haihuwar ce. Kowa ya cika da mamaki. Yabi likitocin da nurses ya zage su tas. Domin da da akwai karar kwana data rasu.

Gashi ta jigata tana ta salati, Can ta janyo surah ta shiga Karantawa tana kuka. Takasa haihuwa da kanta. Daga karshe likita yace mijin yasa hannu ayi aiki a ciro. Saifuddeen nata tsiyayar hawaye haka yasaka hannu aka shiga da Maimunatu dakin tiyata tanata karatun alqur □□ ni tana kuka da karfi. Basu dau lokaci sosai ba aka fito da katon jariri.

□□ na mahaifin sa, Gashi nan kayi masa huduba, Zamu dan yi masa checkup dan shi bai zo da lapia ba gaskia.□□

Hannun Alhaji saifuddeen na rawa ya karbi jaririn yana hawaye. Huduba ya masa yana mai matsa masa ruwan dabinon daya tofa a baki.

□□ aku iya ganinta.. Dan zamu mata allura ne. Batada lapia sosai.□□

Duk suka dunguma suka shiga cikin dakin. Tana kwance tana hawaye. Bakin ta dauke da karatun qur □□ ni tana yi a hankali. saifuddeen ya karasa kusa da ita yana dan nuna mata jaririn.

□□ aimunatu nahh! Ashe yan biyu ne. Mun kara samun albarkar wani □□ an namiji. Tsiran su kwana biyu da wuni. Na rad □ □ masa MUHAMMAD HAFEZ. HAFEZULLAH!, Hafizin qur □□ ni ne Insha Allahu, Saboda haihuwar sa mai abin mamaki ce. Da karatu a bakin ki kikai nakudar sa.. Allah ya raya mana su. HABEEBULLAH DA HAFEZULLAH!□□

Jikin ta gaba d □□ ya sai ya soma rawa. Tana mika hannunta ya bata. Tana karba ta saki wata kara. Kafin tai wulli dashi gefe. Kowa ya dimauta da ganin abunda ya faru. Likitoci sukai kanta suna bata taimako. Ashe wata sabuwar jijjigar ce. Tasha wahala ainun. Jaririn ma daukar sa akayi aka shiga bashi temako, Babu abunda ya same shi na buguwar da yayi. Sai dai yazo da ciwon zuciya mai tsanani..

□□
Furgigit ta farka tana gumi duk kuwa da iskar fankar dake kad □□ wa, Ga kuma sanyin ruwan sama.

□□ waggo... !Gwaggo □□

□□ a □□ m diyar albarka.□□
Gwaggo ta farka da sauri daman batada nauyin bacci kwata kwata.

□□ waggo! Ashe yan biyu na haifa? Gwaggo ina Hafez? Hafezullah dana haifa daga baya bayan kwanaki biyu da haihuwar tagwan sa Habeebullah? Gwaggo suna ina? Habeeb da Hafez? Suna ina Gwaggo? Ina saifuddeen? Mahaifin su?□□

Gwaggo ta sauke ajiyar zucia tana hamdala.

□□ abarine mai tsawo Maimunatu. Shekaru da yawa a talatin kadan ne babu. Sannu ahankali sai yanzu Allah ya ida nufin sa hankalin ki da tunanin ki suke dawowa....□□

Wani kuka ne ya kufcewa Maimunatu mai tsuma zuciar duk wanda ya saurara. Haba shi yasa mutane suketa zuwa mata murna. Kuka ta shiga yi sosai harda shessheka. Gwaggo Haule ta mike ta janyo ta jikin ta tana rarrashin ta.

□□ an sanar da ke komai... Idan kika kammala tuno duk abubuwan da suka shude diyar albarka. Yanzu kije kiyi alwala kiyi sallar godia ga Allah daya azurta ki da wannan baiwa. Domin ko acikin mutanen duniya masu irin matsalarki da wuya suke warkewa. Likitoci da dama suna mamakin warkewar ki. Sai dai komai na duniya fararre ne kararre ne. Allah bai saukar da ciwo ba sai da yayi maganin sa. Kedin mai karatu ce. Shi yasa ubangiji Allah ya warkar dake... Sannu diyar albarka. Tabbas kinsha jinya.□□

Mikewa Maimunatu tayi bayan ta gama goge hawayen ta, Taje ta kama ruwa tayo alwala. Ta shiga sallolin godia ga Allah. Duk yan gidan kowa ya fito jin motsin su gwaggon, Nan Gwaggo Haule ta shiga basu labarin abunda ya faru na kwanciyar yau da Maimunatun tayi.....

****MADRID***

Yana daga kwance bayan yasha maganin ciwon zuciar sa. Bacci na neman daukar sa wayar sa tashiga kara. Ganin me kiran yai saurin dauka. □□ NK □□ (Baba kano) Gaisawa sukayi sosai. Alhaji saifuddeen nata tambayar jikin sa. Basu wani jima ba sukai sallama. Ba dadewa kuma Habeeb ya kirashi. □□ B □□ (twin brother)

Dauka yai nan ma suka sake gaisawa dashi bayan wayar da suka yi dazu. Amman wannan karon video call suke ta Skype.

□□ hm!Yanzu mukayi waya da Baba ma...□□

□□ eah yacemin zai kira ka ai... kasha maganin? □□ abeeb ya fada yana mai kallon fuskar Hafez ta waya.

□□ eah na sha..□□

□□ oh ya jikin? Allah Kara sauki □□

□□ amin!! Da sauki □□

□□ ohm bara na ky □□ le ka kayi bacci. A gayda su Aunty.□□

□□ ohm! Zasu ji, Okay! Goodnight □□

Katse kiran yayi. Ya ajiye wayar. Ya dora kansa akan pillow yana lumshe idanun baccin dake fusgar sa..

***Shima Habeebullah a nasa bangaren ya ajiye wayar ahankali yana murmushi. □□BH□□ (Twin brother Hafez) Haka yai saving sunan tagwan nasa da shi.

□□ ammaa! Allah ya Kara baki lapia, Yasa muna da rabon ganawa da ke. Allah ka cikawa Hafez da ni burin mu na ganin Mamma..! Allah kuma ya kara hada kawunan mu ya toshe duk wata □□araka da zata taso..□□

Cike da farin ciki ya janyo files din gaban sa yana mai dudduba su.....

□⑩€⑩€⑩€⑩€⑩€⑩€□□

Ni kai na Nana Hafsatu sai dana matse hawayen farin ciki, Allah ya raya mana ku. MUHAMMAD HAFEEZULLAH SAIFUDDEEN IBRAHIM SANDAMU DA MUHAMMAD HABEEBULLAH IBRAHIM SANDAMU...!!! □□□□□□□□□□□□ YAN GIDA DAYA, YAN BIYU MASU KAMA DAYA, MASU HALI MABAMBAMTA □□□□□□□□□□
Tab ruguntsumi □□Ya zata kaya ne?□□□□ Waye zai hakura.... ?□□□□□□□□□□□□□□€□□□□ ohoho □□□□□□

□⑩€□□
Ba lalle na cigaba da posting kullum kamar yadda na fara ba, Zan dan dinga hutawa kamar na zafafan baya. Ido ya fara matsawa.
Muna godia da kaunar books dinmu da kuke □□□

*_□□ AL-□IBLA_*□□
Na Safiyya Huguma

*_□□ MABU□IN ZUCIYA_*□□
Hafsat Rano

*_□□ DALAAL_*□□
Na Miss xoxo

*_□□ UBAYD MALEEK_*□□
Na Mamu gee

*_□□ MAKAUNIYAR □ADDARA_*□□
Na Bilyn Abdull

Lalai daga ji babu tambaya bana ma ZAFAFAN ku da turirinsu suke tafe. Dan dagani kasan za'a ragargaza cakwakiya, soyayya. Tare da nisha □i □□□□□□□□□□□□□□□□□.

Gasu duka akan farashi mai rahusar gaske.

Kamar haka □□□□□□□□

□aya___300
Biyu____400
Uku_____450
Hu□u____500
Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki □□□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban ta whatsapp shedan biyanku(evidence of payment/Account name)□□□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU □□□□

□ 0903 □ 234 □ 5899

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
TEAM----ZAFAFA BIYAR □□□□□□□□
10/17/21, 2:11 PM - Aisha Adam: *NH*

19

*Abdul-rahman (sudais) is a young boy who's so passionate about putting the Holy Qur'an into memory. Please help this little boy grow his YouTube channel *ABDUL-RAHMAAN* you got nothing to lose in sha Allah thank you and Jazakumullah khair □ □□□

https://youtu.be/WWIGq5Jbtb0

Do subscribe please...

*DAN ALLAH A SHIGA A DANNA SUBSCRIBE DON GANIN DUK SANDA AKA DORA BIDIYON SUDAIS YANA KARATU, HAFIZIN YARO NE DAYA TASO DA ZUCIAR SON KARATUN ALQUR □□ NI. *

JAZAKUM ALLAH KHAIRAN AS YOU SUBSCRIBED □□□□□□

DALAAL

Tana kwance akan cinyar Ummy. Ummyn na shafa mata kanta, Sai lumshe idanu take bacci na son daukar ta. Can ta daga kai tana duban Ummy.

□□ mmy! Habeeb yacemin yanada brother da baya gidan nan da a Morocco wai yake. Toh kuma ni a Spain na taba ganin wani me kama da Habeeb din. Amman kawai yanayin fuskar sa da sajen ne sai tsawon da yanayin jikin. Saboda banga kwayar idanun sa ba. Lokacin yana sanye da glasses.□

□□ a □□ m hayateey! Zahiri. Tabbas Hafezullah kanin Habeebullah ne, Yan biyu ne. Shi Hafez din yana wajen k □□ nwar mahaifin su dake aure acan, Ko sanda aka auro ni gaskia banzo na tarar da shi ba. Sun dai taba zuwa wai Shi da Haj ziyadan, Lokacin ni kuma naje kaduna. Tabbas a madrid Alhaji yacemin suke da zama.. Ai kuwa suna kama sosai.□

Shiru Dalaal tayi na dogon lokaci. Gaba d □□ ya ta rasa kalmar da zata furta. Ashe dai idanun ta ba gizo suke mata ba? Ajiyar zuciya ta sauke.

□□ llah sarki...□

□□ enene Hayateey?□

□□ abu komai Ummy! Kawai ina mamaki ne ashe yan biyu. Gaskia suna kama. Dan dai wancen yafi wannan hasken fata.. Wacece maman su to?□

□ □ dentical Twins ne tabbas, Mahaifiyar su bata gidan nan ai, Haj Binta itace marikiyar Habeeb. Ita kuma Haj Ziyadah itake rikon Hafez. Mahaifiyar su kauyen su d □□ ya da babansu Habeeb din. Sunan ta Haj Maimuna..□

□□ llah sarki! Da an sani ba □□ raba su ba..□

□□ oh ya za □□ i? Akwai dalili shi yasa.□

□□ oh Allah rufa asiri.□

□□ amin Hayateey. Ya zancen yajin aikin?□

□□ onday me zuwa za □□ tafi.□

□□ aboda hafsatu ta ishe ni, Da zuwan ki.□

□□ anje Insha Allah.□

Hira suka cigaba da yi. Gwanin ban sha □□ wa. Dalaal kawai dai dauriya take. Amma lamarin ya d □□ ure mata kai. Gashi kwanan nan tunanin sa na neman birkita mata lissafi.

SANDAMU

Haj Maimunatu gaba d □□ ya cikin tsukukun nan ta kasa cin abinci sosai, Gaba d □□ ya maganarta d □□ ya biyu akan yaranta suke. Data fara tunani kuma kanta zai soma ciwo.

□ □ waggo na kasa tuno komi fa, Abunda na iya tunowa shine kamar na dan fara shayar da su suna jariran ko? Toh ni dai iya nan na iya tunowa. Kayan Habeebullah na jarirai shud □□ ne, Shi kuma na Hafezullah kore ne...□

Gwaggo Haule na daga gefe itada Hadizalo. Hadizalo na gyaran kayan miya, Ita kuma gwaggon tana goga goro a magogi. Gwaggon ta nisa tana mai zura goran data bare a dan tofin dake cikin ta.

□□ ahiri....Anyi haka diyar albarka, Kin shayar da Habeebullah da Hafezullah kusan kwanaki nawa nema idan ban mance ba. Suna jariran. Alokacin bayan kin haiho Habeeb mun dawo gida ruwan mama bai zo maki ba. Saifuddeen ya hiddo kudi aka siyo madara aka damawa Habeebulla. Daga nan ma ciwo ya dawo sabo, Ashe nakudar Hafezullah ce. To bayan kin haihe shi. Sai jijjiga tazo miki. Kin sha wahala ainun. Har takai kinyi jifa da Hafezullahi.□

Haj Maimunatu ta rintse idanu tana hawaye, Hade da jijjiga kai tana salati.

□□ waggo ki bar zancen nan.□□
Hadizalo ta fada tana zubar da hawayen itama.

□□□□ h Gwaggo cigaba inason ji., Dan Allah karki b □□ ye min komai □□

Gwaggo ta fyace hanci tana mai cigaba da cewa.

□□ oh sai likitoci suka shiga baki temakon gaggawa, aka duba Hafez aka ga buguwar batai masa komai ba. Sai dai kwana biyun da yai da yini, Bayan kin haihe tagwan sa. Da jijjigar da kika yi. Da wasu bayanai dai da likitan ya fada. Shi Hafez sai yazo da ciwon zuciya. Dan gaskia har ranar da zasu karb □□ su ma sai da aka kaishi asibiti.□□

□□ waggo! Meyasa aka karb □□ su.□□

□□ aimunatu dole a karb □□ su. Tunda kinga matsala kika samu. Har takai ki kanyi jihwa/jifa dasu karo na biyu kenan. Akan kuma idanun baffannin shi saifuddeen da kannen mahaifiyar sa mata. Matsala ce data samu kwakwalwar ki da tunanin ki. Tunda kowa mance shi ki kai. Yaran ki kai jihwa dasu bayan an dawo gida kina basu Mama. Shi kanshi saifuddeen idan yazo ganin ku daukar abu kike ki je hwa masa...□□

□□ auka dai nayi sosai Gwaggo.□□

□□ iyar albarka... Ki godewa Allah! Domin kinsha jinya gaskiya. Domin ni da kannen mahaifiyar sa mu kayi shawara kan lalle ya karo aure. Idan yaro ya isa yaye ya bawa matar shi. Ko ita ta shayar da shi. Domin kinga ni na manyanta ba zeyiwu na shayar dasu ba. Ga ki ke babu dama sai a cutar dasu. Shikenan sai akace akwai kanwar sa datayi aure da dadewa bata taba haihuwa ba. Nan mukai shawara kan sai a bata d □□ ya itama.□□

□□ iyadatuh?□□
Haj Maimunatu ta tanbayi Gwaggo tana mai goge hawayen fuskar ta.

□□ abbas itace kau! To dai gaba d □□ ya sai aka cigaba da basu madara. Da akan kawo sunan din Idan kina bacci a sakala musu maman su sha. Idan kika farka sekita bori kina fashe fashe. Daga karshe ma duk sanda Za □□ kawo su ko idan shi saifuddeen din yazo sai abin naki yayi tsamari ki wuni kina kuka bakyason ganin su baki d □□ ya. Har kwana yake a bakin kofar gidannan sau ba adadi yaron kirki. Na kira Alhaji Aminu nace ya nemi manyan saifuddeen din kan ya sawwake miki. Domin aure ba zai yiwu a haka ba.

□□ ak □□ ar dai ya iya shikar ki, Shika d □□ ya ya miki. Yara kuma aka bawa ziyadatun Hafez, Shi kuma Habeeb wata gwaggon su ta karb □□ shi. Basu shekara biyu ba saifuddeen din aka daura mishi aure da wata diyar abokin baban sa. Toh yarinyar kirki dai wallahi ita ta cigaba da shayar da Habeeb har Allah ya temaka aka yaye shi. Shi kuma Hafezullah yaki amsar maman Ziyadatun, Har wajen mutane ukku duk yaki amsa. Sai madara suka cigaba da bashi. Dakyar yake iya karbar maman, Daya karba zai saki. Inaga sau biyu akace yasha na ita ziyadatun. Dake Allah ya sanya mai garin jiki ne kuma mai kwana agaba ne sai Allah ya raya shi.

□□ a anan garin kanon ita ziyadan take. Kullum sai takai Hafez wajen Habeeb har suka taso suna tafiya da magana. Sun yi sa □□ r marik □□ gaskia. Sun rike su da

amana. Duk sanda za □□ kawo su wajen ki to fa ranar ke ba Lahia kinta yage yage kina doke abubuwa. Ganin haka yasa nace saifuddeen ya dena kawo su. Nan gaba zasu kawo kansu idan sunyi wayo. Gida da komai haka saifuddeen ya bamu a kano kan mu koma, Nace a □□ h! Ya dai barmu nan din. Har Allah ya baki lahia ki koma dakin ki idan kin amince.

□□ oh ana haka. Jikin Hafez sai ya matsa lokacin yana shekaru hudu ne ko uku. Bazan mance ba saifuddeen ya kara zuwa yana sanarmun kan su ziyadan zasu bar kasar kuma da Hafez zasu tafi Zai dinga ganin likita acan. Toh hakan akayi. Suka tafi kasar Morocco acan ya zama hafizin gaske har ya haddace qur □□ ni cikin kankanin shekaru ko nawa ne na manta. Amman dik hutu sai yazo shi wajen tagwan sa. Shima tagwan yakan je wajen sa. Toh haka dai suka cigaba da rayuwa.

□□ hi Hafez na can kasar Shi kuma Habeeb yana nan, Har Allah ya azurta marikiyar sa da haihuwa itama. Tafara haihuwa, Yayanta ko nawa ne an fada na mance don munje radin sunan ma. Toh Shi dai Habeeb ya kanzo nan din a boye don Karki gani. Shi kuma Hafez yana can yana ganin likitoci. Sun zagaya k □□ rashe da dama. Itama marikiyar tasa na neman haihuwa. Daga karshe ma dasa mata akayi. Ta haifi mace bayan Hafez din ya girma abadan ma. Sai suka koma kasar turawa kuma nan ma aka kuma dasa mata wani cikin ta sake haihuwar mace. Ance bata kara zuwa an dasa mata ba, yaran nata na nan kanana guda biyu.

□□ hi Hafez gaskia Saboda yanayin raunin zuciar sa ba □□ so yaga halin da kike ciki Shiysa mahaifin nasa ya hana kowa ya kawo shi wajen ki. Nima kuma na goyi bayan hakan ganin shid □□ n bame lahia bane. Amman dai Habeeb har wasu yasaka a boye suke duba lahiar ki Idan kin fita. Sannan shi mahaifin nasa yana mana aike gaskiya sosai, Ya samawa wannan dan (Malam Bala) aiki acikin birni. Sannan marikan Habeeb da Hafez din suna kokarin aiko kayan abinci da suturu a kawo miki. Hajiya binta marikiyar Habeeb wallahi har kayan abinci da kudi a boye take bayarwa akawo.

□□ mman dai Hafez saboda yanayin ciwon sa shi bai kara sanya ki a idanun saba. Habeeb yacemun Saboda hakan ne ma yake fushi dasu duka. Kan boye masa da ake. Amman yanzu Alhamdulillah za □ □ ita baki dafa □ □ kicigaba kuma da shan magungunan ki na asibiti. Likitoci na kara duba ki. Ga sauka ana miki da yardar Allah komai yazo karshe. Saifuddeen dinma yace zasu zo. Idan kika huta. Nake jin har Hafez dinma dan ance ya kafe sai ya dawo kasar nan. Ki godewa Allah Maimunatu, Yaran ki nutsattsu ne, Sun tashi a hannu na gari, an rike su kamar □□ a □□ a. Ba suyi maraicin uwa ba . Sun samu uba nagari jajirtacce. Habeebullah babban lauya ne na fannin shari □□. Shi kuma Hafez din ance dakta ne na ilimi fannin kwamfuta... Alhamdulillahi.□□

Haj Maimunatu ta matse hawayen farin ciki,

□□ waggo shekarar su nawa yanzu?□□

□□ asu kai talatin ba. Amman dai a deb □□ namu na hausa. Muga..□□

Ta shiga irgawa da hannu tana lissafi can ta cigaba da cewa,

□□ turance 28 suke, A debe na hausa sunyi 29.□□

□□ llah ya raya su..□□

□□ amin Yaa rabbi.. Aamin.□□

□□ waggo kina ganin zasu yafemin?□□

□□ afewa wacce iri? Me kikai musu? Ke din da ba a sane kike komai ba, A haihuwar tasu fa kika ha□□u da wannan lalurar diyar albarka.□□

□□ oh Gwaggo ku yafemun..□□

□□ abu abinda kikai mana diyar albarka. Sai da ma ince dake ki yafeni saboda ni ce na bada shawarar a dauke su. A kuma raba auren naku zuwa sanda zaki warware.□□

Hawaye ta shiga gogewa tana salati. Sai da tayi kukan ta mai isarta sannan tace da Gwaggo

□□ waggo shawarar da kika basu itace wadda tafi dacewa, Ko nice nan kwatankwacin haka ya faru da wani nawa shawarar da zan bayar kenan. Alhamdulillah! Allah na gode maka. Allah ka yalwatawa bayin ka lahia ingatacciya.□□

□□ llahumma Aamin diyar albarka, Hadiza sauke ruwan wankan nan ki sirka ki kai mata bayi. Diyar albarka tashi ki wanka ko kyaji dadin jikin ki. Kizo ga tofi Malam ya aiko almajirin sa. Idan Kinci abinci kuma ki hadiyi magungunan ki.□□

□□ oh Gwaggo.□□

Bata musa ba ta mike ta zura hijabi ta cire kayan jikinta ta daura zani. Hadizalo ta kai mata ruwan wankan, Bayi ta shige ta fara wanka. Tana yi tana hawaye...

MADRID

A nutse ya karasa parking din motar a parking lodge. Ya shige cikin gida bakin sa dauke sallama.

□□ a dawo Hafez? Duk kowanne ya shiga□□

□□ a dawo Maa! Eh kowanne yayi. A daren yau ma za□□ sasu a jirgin da zai tafi lagos direct.□□

□□ asha Allah! Kaga ai mun samu sauki, Sai yan kayayyakin da suka rage kawai. Yaya kuwa ya kira wo ka?□□

□□□□ h!□□

□□ h okay...□□

□□ ani abu ya faru ne?□□

Murmushi Haj Ziyadah tayi tana mai girgiza kanta,

□□ bun farin ciki ne, Nasan ko shi bai gaya maka ba, Habeebullah zai gaya ma.□□

Murmushi yayi kawai yana adduar Allah yasa mafarkin sa ya zama gaskia. Dan kwanakin nan sai yaita mafarkan wai sun hadu da mahaifiyar su.

□□a abinci a dinning. Kar ma ka soma cemin ka koshi, Dan sai ka ci.□□

Dinning din ya nufa, Ya zauna ya debi abincin a plate ya naci. Yana kammalawa ya haye sama. Wanka yayo ya zura doguwar rigar jallabiya. Kwanciya yai akan gado bayan ya kunna karatun qur□□ni. Qira□□r sudeis sai tashi take. A hankali yake bin sudeis din daki daki. Cikin haka wayar sa tayi kara, Hanzarin dauka yayi yana mai tsaida karatun.

□□aalykm Salam! Lapia qalau...! Ya naka? A□□h bai kira ni ba. Oh Eh na kai kayan mune airport. Mu sai monday zamu taso Insha Allah. Mu sauka a lagos. Sai mu taho abuja kuma Maa Zata karba sak□□awajen k□□warta. Washegari sai mu taho kano. No banda Papa. Shi Luxembourg zai tafi. Sai daga baya ze biyo mu ... Me kace?□□

Mikewa Hafez yai yana dafe saitin zuciar sa. Hawayen daya ke kokarin maida su suka shiga zurarowa. Zubewa yai a kasa. Saboda gabadaya jijiyoyin jikin sa sun saki.. Bakin sa na rawa yashiga tambayar Habeeb, Kana jiyo muryar Habeeb din yana ta kirawo sunan Hafez.

□□ro! Kai Hafez! Hafezullah! Ba dai jikin bane ko?□□

Ina Hafez ai cire wayar yayi daga kunnen sa ya dubi gabas yai sujjadar godia ga Allah.

□□ello...! Ina jinka bro.. Sorry sujjada nayi. Kasan inata mafarkai kusan yanayin haka? Alhamdulillah Yaa Allah!□□

□□allahi! Alhamdulillah! Allah ya kara bata lapia.□□

□□amin..!□□

□□hikenan bari na barka ka huta...□□

□□kay! Godia nake..□□

*_□□ UBAYD MALEEK_*□□
Na Mamu gee

*_□□ MAKAUNIYAR □ ADDARA_*□□
Na Bilyn Abdull

Lalai daga ji babu tambaya bana ma ZAFAFAN ku da turirinsu suke tafe. Dan dagani kasan za'a ragargaza cakwakiya, soyayya. Tare da nisha □ i □□□□□□□□□□□□□□□□□.

Gasu duka akan farashi mai rahusar gaske.

Kamar haka □□□□□□□□

□ aya___300
Biyu____400
Uku_____450
Hu □ u____500
Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki □□□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban ta whatsapp shedan biyanku(evidence of payment/Account name)□□□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU □□□□

□ 0903 □ 234 □ 5899

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
TEAM----ZAFAFA BIYAR □□□□□□□□
10/22/21, 10:24 PM - Buhainat: _DALAAL □□□_
A new world/Destiny □□ love

_54_

ZAFAFA 2021
BOOKS DIN KUDI NE.

RANO NET! RANO NET! RANO NET!

WHO NO LIKE BETA AWUUF THINGS?

IDAN KAJI GANGAMI DA LABARI....! INA MASU ZUBIN ADASHEN DA BA RANAR DAUKA NA DATA?

TO KU MARMATSO KUJI, KU KUMA SHARE HAWAYEN KU, MUNZO MUKU DA SABBIN TSARE TSARE NA DATA, WADDA KOWA ZAI IYA SAYA DAI DAI KARFIN SA. A FARASHI MAI RAHUSA

_RANO NET! RANO NET! RANO NET!__
(Afford data at chikini price)
MALLAKI DATA A KUDI KALILAN DA RANO NET

TSAYA KUJI, A RANO NET ZAKA IYA ZAMA RESELLER KO WHOLESALER KAI MA, EH ZAKA/KI IYA ZAMA MA SAYAR DA DATA A FARASHIN SARI MUKE BAYARWA, KAI/KI KAFA KASUWANCIN KU KUMA. DA KUDI KALILAN.

MUNA KUMA SAYARWA AKAN □□AI DAYA, KOWANE NETWORK MUNA SAYARDA DATA PLAN DINSA AKAN KUDI KALILAN, MASU FARASHIN SARA KUWA MA KU KUDIN BAI KAI HAKA BAMA

AIRTEL
9MOBILE/ETISALAT
MTN
GLO

DUK MUNA SAYARDA TSARIN DATA DINSU. KAMAR MISALI MTN MUNA SAYARDA 1GB.24MB AKAN FARASHIN NERA 300 KUMA YANA KAIWA WATA DAYA, GWARGWADON YADDA KAKE AMFANI DA DATA, 2GB 600, 3GB 900!!

DUKA WADANNAN TSARIN DATA DAMA NA SAURAN LAYIKA MUNA SAYRWA AKAN FARASHI MAI RAHUSA, WANDA KOWA ZAI IYA YIN TSARIN DAI DAI ALJIHUN SA

Ranonet.com.ng
_GA SITE DINMU NAN DAKE YANAR GIZO, KAI TSAYE ZAKI/KA IYA SIYAN NAKA TA NAN. _

KO A TUNTUBE MU TA NAMBAR TARHON MU: +234 □ 803 □ 081 □ 1300/+234 □ 808 □ 540 □ 5215

KYAU, INGANCI, RAHUSA, ADADE ANA YAWO A YANAR GIZO SAI RANO NET.

RANO NET..!!!!

HABEEBULLAH □□

**Tunda ya dawo daga masallacin sallar asubah ya mike akan kujera yana jiran fitowar ta. Sam daren jia sai bacci □□arawo ne ya dinga sace shi, Idan ya □□an yiyyi sai kuma ya farka. Shysa daya dawo daga masallaci ya mike a kujerar bayan ya dan bubbugawa Dr. Nabeelah dakin yana marairaice mata,

□□iyi hak□□ri....My Queen.□

Wata doguwar hamma yayi, Ya dan rufe bakin nasa yana karkade pillown kujerar. Ya sake mik□□wa yana lumshe idanu. Take bacci barawo ya dauke shi.

Nabeelah bayan ta idar da sallah ta shige ban□□aki tayo wanka. Shryawa tayi cikin manyan kaya. Atamfa doguwar rigar A line. Ta daura dankwali hade da yafa wadataccen mayafi akanta.

Dan lekawa tayi ta hudar kofa. Nan ta hango Habeebullah a kwance da alamu kuma bacci ya dauke shi. Da sand □□ ta sauka kasa. Hannunta rike da takalmanta da jakarta.

Kitchen ta nufa kai tsaye bayan ta ajiye takalman ta da jaka a parlor. Dankali ta fere tanayi tana kallon agogon dake d □□ure a wutsiyar hannun ta. Bata dauke lokaci mai tsawo ba tagama suyar dankalin. Ta kada kwai shima ta soya shi. Ta hada da flask din tea da kayan shayi da ketchup, Da bread, Ta kai masa komai parlor ta jere. Na Lawwali mai gadi ma ta zuba masa a yar kular da ake zuba masa abincin sa. Ta dora masa nasa biredin akai. Jakarta ta rataya a kafada. Dayan hannun kuma ta rike abincin Lawwali. Ta zura takalmanta ta bude kofar ahankali ta fita. Lawwali ta bawa abincin sa. Ya bude mata gate din. Ta fita da motar ta, Kai tsaye ta wuce asibiti.

Habeebullah cikin bacci kunnuwan sa suka shiga jiye masa karar turin gate. Ya dan bude idanun sa ahankali yana kikkifta su. Da sauri ya mike yana addu □□. Dakin Nabeelah ya gani a bude kuma bata ciki.

□□oney pie! Honey pie....□□

Ya shiga doka mata kira yana dudduba sauran d □□kunan biyu dake sama. Har da bandakuna da ma □□jiyar tara kayan wanki duk sai daya duba. Ba Nabeelah ba alamar ta.

Kasan ya sauka. Tun daga kafar bene ya shiga hango jerin kwanukan abinci, Ya karasa sauka yana kallon ko □□na na parlorn. Kafin ya bude daya kofar parlorn ya shiga. Ba tanan. Dakin dake cikin parlorn ma bata nan.

Komawa parlron tsakiya yayi. Ya zauna akan kujera yana zabga tagumi da hannuwan sa duka biyu ya rike habar sa. Can ya kalli agogo ya mike ya shige dakin kasa. Wanka yayi a bandaki ya tsaftace jikin sa sosai. Shiga yayi cikin kananun kaya. Ya feshe jikin sa da turaruka masu karfin kamshi. Wayar sa ya cire daga jikin chargy ya riketa a hannu.

Parlorn ya koma. Ya debi dankalin da kwan a plate. Ya shiga ci yana dangalar ketchup. Yana korawa da flavored tea din vanilla. Yana kammalawa ya mike yana hamdala. Tattara kayan yayi ya kai kitchen, Ya dauki mukullin motar sa ya fuce daga gidan. Bayan ya kullo shi.

□□allabai barka da fitowa. An tashi lapia?□□

□□apia Alhamdulillah Lawwali. Kana lapia?□□

□□apia kalau yallabai.□□

□□asha Allah! To mun fita.□□

□□llah ya bada nasara Yallabai. Ya kai ku lapia ya dawo mana daku lapia. Allah ya bunkasa ya kuma yalwata arziki.□□

□□llahumma Aamin. Muna godia.□□

Mota ya shiga ya tayar. Da addu □□ ya fuce da motar yana dagawa Lawwali hannu. Har ya fara tafiya ya gangara bakin titi ya faka yana janyo wayar sa a aljihu. Kiran Nabeelah yayi har sau biyu bata daga ba. Ya wuce wajen aiki. Can ma ya shiga

kiranta ba kak □□ autawa. Nan ta maida masa da sak □□ n: Tana emergency ne suna wa wani surgery ba da □□ ewa suka fito.

Hamdalah ya sauke yana murmushi. Ya shiga zana mata message fuskar sa kumshe da farin cikin kasancewar Nabeelah a matsayin matar sa,

□□ aving a doctor as your wife means double the care of your health and fitness □□. I am truly blessed to be your husband □□. Allah ya cigaba da baku sa □□ da hakurin juriyar duba marasa lapia. Ina sake miko kokan barar ban hakuri dai akan kuskuren da nayi jiya. I love you soo much.□□

Ya tura mata yana mai cigaba da dudduba tarin files dake gaban sa. Dr. Nabeelah na zaune tana hutawa akan kujerar dake office dinta. Fitowar ta daga surgery kenan tana hutawa ba dadewa da mayarwa Habeebullah sakon tana surgery ne, Reply dinsa ya shigo karantawa tayi tana murmushi ta ajiye wayar a gefe. Hade da mikewa ta fice ward check.

□⑩€⑩€□. □⑩€⑩€□. □⑩€⑩€□. □⑩€⑩€□.

**Yana tashi daga office gida ya wuce, Nabeelah bata dawo ba. Kai tsaye ya shige dakin sa. Ya sake yin wanka saboda yadda rana ta dake shi dazu daya biya gidan gonar su. Shiryawa yayi cikin jallabiya ya dora hula akan sa. Ya sake fita bayan ya bawa Lawwali dari 3 yace ya siyo abinci.

Ya tsaya a wata plaza ya karb □□ sako, Kai tsaye ya wuce asibiti wajen Nabeelah. Yana shiga yaci sa □□ tana office dinta ita kadai. Tana duba system din dake gabanta.

□□ ssalamu Alaikum!□□

□□ aalykm Salam □□
Ta amsa shi tana dan daga kai ta dube shi.

K □□ rasawa yayi ya zauna a kujerar dake fuskantar tata yana zuba mata manyan idanun sa. Cikin wata iriyar murya a raunane yace,

□□ a aiki...?□□

□□ lhamdulillah! Ya naka?□□

□□ lhamdulillah!□□

Wani kwali ya ajiye mata agabanta. Yana hada hannuwan sa biyu waje d □□ ya alamar ban hakuri. Kamar ba zata duaka ba, Sai kuma ta bude kwalin mai dauke da letter donuts. Donuts din an musu shape din haruffa. A jere kowane an masa hadi. □□□□ very sorry dear wife.□□

Murmushi tayi tana kallon donuts din. Kafin ta daga idanunta biyu ta narkar dasu akan sa.

□□ a yadda kayi lefi kenan... Ka amince ka sab □□ alk □□ wari ko?□□

□□ a amimce... Tun jia danaji ajiki na na tabbatar ni me lefi ne. Na kuma karbi lefi na da hannu biyu. Toh a dan murmusa mun na tabbatar an huce....Kinji?□□ Yadda ya

karasa a lankwashe kamar zai mata kuka ne ya sanya Nabeelah sakin dariyar da bata shirya ba.

Yayi murmushi yana sake bin ta da kallo cike da kauna. Ahankali Nabeelah tasa hannunta ta dauki guda d□□ya tana ci tana yaba dadin sa.

□□ayi dadi sosai...□□

□□aji dadi ya miki yadda kikeso, Sai dai har yanzu baki ce kin huce ba.□□

Donut din daya ta dauka ta mika masa. Ya karba hade da sumbatar hannunta data miko masa.

□□odia nake....So nake na tabbatar an huce din kuwa?□□

□□ai ai ba □□ fushi da kai na tsawon lokaci. Ko mutum yayi niyya sai ka san yadda kayi ya sauka. Na hakura mana, Kawai dai naso kwana a gidanne kamar yadda ka alkarwanta. Sai kuma ka sab□□, Abunda yaban haushi sosai ma shine tun kafin na tafi sai kacemun bafa kwana zan ba, Ko kuma danaje din bayan na rakaka wajen mota nanma zaka iya cemun kar na kwana na dawo karfe kaza. Ko kayo mun message. Kaga yan gidan mu zasu dauka zance na na ha□□a ni ce meson na kwana... Shine kawai abinda ya konar rai.□□

Har ta karasa kallonta yake. Tana gama magana ya dakko ruwa ya mika mata yana murmushi,

□□oh kiyi hak□□ri.... Ungo ruwa ki sha ya sanyaya miki zucia. Nayi lefi gaskia sosai. Musanman kan sab□□ alkawarin da nayi. Insha Allah nan gaba haka ba zata sake faruwa ba. Tuba nake ranki ya dade.□□

□□a wuce tuntuni.....Yau ba su karramammiya din?□□

Yayi murmushi yana girgiza kai,

□□abu su yau... Abinda kikeso shi kawai za□□y.□□

Nabeelah tayi dariya tana girgiza kai,

□□oh Yallabai....Bara na duba wani patient dina. Sai nazo mu tafi.□□

Ta mike zata wuce ta kusa da Habeebullah ya riko hannunta shima yana mikewa tsayen.

□□abeelah..... Ina kaunar ki sosai, Allah ya dawwamar da zukatan mu cikin kaunar juna, Ya kauda duk wata fitnah a tsakani.□□

□□amin Aamin.□□

Sakin hannun nata yayi, Ta fuce tana janyo kofar. Shi kuma ya koma ya zauna yana dudduba wayar sa.....

_*ZAFAFA 2021! NEXT LEVEL_*
_*ZAFAFA 2021! NEXT LEVEL_*
_*ZAFAFA 2021! NEXT LEVEL_*

□ □ □ □ □ □ □ □

□ □ □ □ □ □ □□□□□□□□□ □□

_*INA MASOYA MAKARANTA ZAFAFA BIYAR MASU SON SAI ZAFAFA SUNYI NISA ZASU SAYA? TOH KU MATSO, DOMIN ZAFAFAN LITTATTAFAN NAKU SUNYI NISA, DAI DAI DAD'IN KARATU_*

_*YAN BIYAR DIN NAKU KAMAR KO YAUSHE SUNA TSAKA DA RUBUTA DADAD'AN LITTATTAFAN SU MASU TAFIYA A TSARE, CIKE DA FADAKARWA, NISHADANTARWA DA KE TAFE DA RANTSATTSIYAR KAUNA MARAR GAURAYE.._*

_*SHIN YAR KUWA KINA DA LABARIN ZAFAFAN WANNAN KARON MA KUDIN SA NA PAGES NA YADDA YAKE KAMAR NA BAYA? DUKKA LITTAFAN BIYAR DIN BABU NA YARWA, KOWANNE DA KALAR DADIN SA_*

□ □ □ □ □ □ □ □ □ □ □ □ *1*

_*DAGA TASKAR SAFIYYAH HUGUMA: WANNAN KARON TA ZO DA WANI SABON SALON LITTAFINTA MAI SUNA : *ALKIBLA* *(THE BATTLE OF LOVE) WANDA KE KUNSHE DA FADAKARWAR RAYUWAR SAMARI DA YAMMATAN YANZU, AKWAI RANTSATTSIYAR KAUNA DA KE WATANGARIRI DA ZUKATAN MUTANE BIYU: ZAHRA DA ALIYUU □□□□□_*

□ □ □ □ □ □ □ □ □ *2*

_*SAI DAGA ALKALAMIN HAFSAT RANO, WANNAN LEVEL DIN TAZO DA NATA KALAR RUBUTUN MAI TAKEN: MABUDIN ZUCIYA! (LOVE/HATRED) MABUDIN ZUCIYA NA TAFE DA FADAKARWA AKAN HAKKIN GASKIYA DA AKASINTA, CAKWAKIYA CE DAUKE DA LITTAFIN WANDA WARWARAR SA NA GA ZUKATA BIYU, RAFEEQ DA AYSHA □□□□_*

□ □ □ □ □ □ □ □ □ *3*

_*DAGA ALKALAMIN MAMUH GEE! WANNAN TAFIYAR TAZO DA NATA SALON MAI SUNA: UBAYD MALEEK(ROYALTY/LOVE) WANNAN KARON KASAR ETHIOPIA TA SHALLARA TA DAKKO AL'ADUN SU MAI CIKE SA FADAKRWA, MUSANMAN AKAN ZAMANTAKEWAR AURE, YA ZATA KAYA NE GA SOYAYYAH GA SARAUTA? WANNAN AMSAR NA WAJEN UBAYD DA NURU!□□□□_*

□ □ □ □ □ □ □ □ □ □ *4*

_*SAI DAGA ALKALAMIN NANA HAFSATU (MISS XOXO) WANNAN KARON TAZO DA NATA TAKEN LITTAFIN MAI SUNA: DALAAL! (A NEW WORLD/DESTINY's LOVE) LITTAFIN NA DAUKE DA FADAKARWA MUSANMAN DANGANA DA HAKURI, YA ZATA KAYA NE DA SOYAYYAR ZUKATU UKU, HABEEBULLAH TAGWAN (TWIN) HAFEZULLAH, GEFE DAYA GA DALAAL DA AKEYI AKANTA?SHIN WA ZAI YARDA YA BARWA DAN UWAN SA?□□□□_*

□ □ □ □ □ □ □ □ □ *5*

_*SAI DAGA KARSHE, BILYN ABDULL! NA TAFE DA NATA SALON MAI SUNA: MAKAUNIYAR KADDARA!!! (BLIND LOVE) LITTAFI NE DAKE DAUKE DA FADAKARWA MUSANMAN KAN KADDARA DA KE FADAWA DAN ADAM, NATA

SALON KADDARAR MAKAUNIYA CE, GEFE DAYA LITTAFIN NA DAUKE DA SALON RANTSATSSIYAR KAUNA AKAN ZINNEERAH... DA BATALIYAR MASOYANTA, MUSANMAN MODIBBO_!□□□□_*

_*DUKA WADANNAN LITTATTAFAI NA ZAFAFA NE DA AKEYI A HALIN YANZU, KUMA KUDINSU NAIRA 700 NE PAGES. DUKA BIYAR DIN. KU GARZAYO KU MALLAKI NAKU TUN DA TURURUN SU, LITTATTAFAN ZAFAFA SUNYI FICE A YANAR GIZO, KU ZO A DAMA DAKU A WANNAN TAFIYAR TA NEXT LEVEL, MASU SANA'OIN HANNU MA MUNA TALLATAWA AKAN FARASHI MAI RAHUSA_*

_*DOMIN MALLAKAR NAKU, KU TUNTUBE MU TA:_*

*_□ AL-□IBLA_*□□
Na Safiyya Huguma

*_□ MABU□IN ZUCIYA_*□□
Hafsat Rano

*_□ DALAAL_*□□
Na Miss xoxo

*_□ UBAYD MALEEK_*□□
Na Mamu gee

*_□ MAKAUNIYAR □ADDARA_*□□
Na Bilyn Abdull

Lalai daga ji babu tambaya bana ma ZAFAFAN ku da turirinsu suke tafe. Dan dagani kasan za'a ragargaza cakwakiya, soyayya. Tare da nisha □i □□□□□□□□□□□□□□□□□.

Gasu duka akan farashi mai rahusar gaske.

Kamar haka □□□□□□□□

□aya___300
Biyu____400
Uku_____450
Hu□u____500
Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki □□□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban ta whatsapp shedan biyanku(evidence of payment/Account name)□□□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU □□□□

0903 234 5899

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
TEAM----ZAFAFA BIYAR □□□□□□□□
10/22/21, 10:26 PM - Buhainat: _*DALAAL □□□_*
(A NEW WORLD/DESTINY □□ LOVE)

_55_

_ZAFAFA2021__
BOOKS DIN KUDI NE. TUNTUBI. ADIRESHIN KASAN SHAFIN DON MALLAKAR NAKA/KI

*YERWA INCENSE & MORE**
(The scents with different essence for YOU& your HOME)

(MASARAUTAR KAMSHI)

INA MASU NEMAN KAYAYYAKIN K □□ MSHI YAN NAHIYAR KETARAN CHADI DA SENEGAL? KAI HAR MA DA INGATACCEN HADI YAN BORNU? TO KU MATSO DOMIN NESA TAZO KUSA...

YERWA INCENSE & MORE: SUN ZO MUKU DA KAYAYYAKIN TURARUKA KAMAR HAKA:

KHUMRA KOWACCE IRI.
TURARUKAN WUTA
MOPPING KHUMRAH
WASHING KHUMRAH
BATHING KHUMRAH
BODY MIST
KULLACCAM
SCENTED HAIR CREAM/SPRAY
WARDROBE BALLS

CARPET SPRAY
AIR-FRESHENERS
SCENTES PEBBLES
BODY SPRAYS
OIL PERFUMES
PERFUMES

KABBASA
ELECTRIC/NON/BURNERS
COAL IGNITER
TONG
KASKO
KUJERAR TSUGUNNO
TURAREN TSUGUNNO
ENGLISH COAL
DILKE&HALWA SET
SCENTED BODY MIST

_KAI DAMA SAURAN KAYAYYAKIN DA BAMU AMBATA BA, YERWA INCENSE AND MORE, NA TURA KAYAYYAKIN SU KO □□ NA A FAD □□ N NIGERIA DA KETARE. DOMIN TUNTUBAR SU, SU NA INSTAGRAM: _@yerwaincense_and_more. Ko

_Facebook site:YERWA _COLLECTIONs. KO A DUBA SU TA NUMBER SU:___08095215215/09044191709! _

MU NA BADA KAYAN MU KAN SARI KO SAYI □□ AI-□□ AI,EH ZAKU IYA SARAR KAYAN MU KO □□ ORA RIBAR KU KU SAYAR.

KYAU, RAHUSA, A DADE ANA AMFAMI DASU, HADE DA INGANCI, KAMSHI GANGARIYA MAI KAMA JIKI DA KAYA DA GIDA, SAI KAYAN TURARUKAN YERWA INCENSE AND MORE

DALAAL

Tana tsaye gaban closet tana danne lebenta na kasa, Gaba d □□ ya jikin ta jin sa wani iri ta ke, Waya ta janyo ta yiwa department head dinsu message kan batada lapia ne ba zata iya zuwa asibitin ba. Towel ne ta daure shi fitowar ta kenan daga wanka. Dan karamin towel din kuma tasa shi tana tsane gashinta. Hafezullah ya shiga tura kofar dakin ahankali zai shigo. Dalaal ta tukwikwiye tawul din, Tana narai narai da idanun ta. Ahankali kamar zatayi kuka tace masa,

□□ an Allah! I want some privacy. Ka juya bayan ka kaji?□

Hafezullah yayi murmushi yana cilla mata wani shu □□ min kallo tundaga yatsun kafarta, Har ya zuwa kanta yake bin kowanne rassa na jikin yana masa kallon □□ urilla. kafin yace,

□□ rivacy? After what we did yesternight you want some pri...va...cy? Meye banga ni ba.?uhm?□

Ya ja kalmar privacy din yana rarrabata hade da lasar kasan leben sa...

□□ i!! ni..ni...ni dai ka fita...□□ a sake fada tana dan bubbuga k □□ fafunta.

Hakan yasanya Hafezullah sakin tattausan murmushi, Ya juya mata bayan kamar yadda taso din. Yana daga hannunsa na dama sama.

□□ afin na kirga goma ki tabbatar kin shirya,D □□ ya...Biyu..Uku..hudu.□ 

Sauri tayi ta janyo zumbulelen hijabi ta zura. Yana kammala kirgawa ya juya ya fara tahowa wajenta cikin takun sa na tak □□ ma da kasaita. Gaba d □□ ya dalaal ta zuba manyan idanunta kansa. Hafezullah a baya sam gani take ko hannu kasa masa a baka ba zai ciza ba. Amman gaba d □□ ya cikin kwanakin nan ta tabbatar wa kanta Hafezullah gwarzon namiji ne. Dan gayu mai addini da Ilimi. Ga iya tarairaya da salon kauna da lafuza. Yadda yake nuna mata so kuwa yanzu lamarin kallon sa take tamkar almara.

Har ya karasa bata saniba. Tayi nisa cikin tunanin sa, Sai ji tayi wata iska mai kamshin mint ta daki fuskar ta da hancin ta.

□□ oorulAyn...□□ a rad □□ mata a kunnenta yana sumbatar kunnen gaba d □□ ya.

Ta tsaya chak tamkar kara. Hafezullah fa ya gama kuncewa yar mutanen Lebanon notina. Ya birkitata da ruwan soyayyar sa. Tsakanin jia da yau ta kasa banbance a wacce duniyar take...?

□□ oorulAyn.. Tunanin me kike ne?□ 

Ya sake kashe mata gabban jikinta cikin wata iriyar muryar sa tamkar ana busa sarewa.

Ganin ta kasa cewa komai, Sai zuba masa idanun ta da tayi, Hakan yasan ya Hafezullah daukar ta gaba d □□ ya ya direta akan gado. Yai mata rumfa da faffadan kirjin sa mai tashin kamshi.

□□ oorulAyn...□□

□□ a □□ m...!□□ Ta amsa shi tana kokarin juyar da kanta gefe.

□□ unya..? Wai kunyar me kike ne...? Um?□□

Ya fada yana kokarin mai do da fuskar ta gare shi, Dalaal ta runtse idanu tana tsuke bakin ta. Murmushi Hafezullah yayi ya sumbaci bakin nata, Yana shafa idanun data rufe cikin wani irin salo na kwarewa. Dalaal tayi azamar mikewa zata gudu, Hafezullah ya dankota ya matseta gam a jikin sa.

□□ atsoraciya... Mena miki?□□

□□ an Allah kayi hak □□ ri...□□ Ta fada ahankali, Hawaye d □□ ya na bin d □□ ya.

Hafezullah ya gyara musu kwanciya. Hannun sa d □□ ya yana shafa bayan ta. Ta jikin hijabin ya lura ya jik □□.

□□ atsoraciya.. Ba abunda zan miki, Kin wanke kan ki ne...?□□

Ta daga kanta a hankali tana sake matse hijabin jikin ta gam.

□□ aki drying ba?...□□

Nanma ta sake daga kan nata. Hafezullahi ya dan janye ta daga jikin sa. Ahankali ya sanya hannunsa zai cire hijabin Dalaal ta rike gam tana girgiza kai,

□□ have the right....□□ Ya fada, Hade da janye hannuwan data rike hijabin gam. Zare hijabin ya shiga yi ahankali har ya karasa cire sa ya ajiye a gefe.

Dalaal daga ita sai towel iya cinya. Ta zubawa zanin gado idanun ta. Don batason ma su hada idanu dashi. Gaba d □□ ya Hafezullah ya kerewa tunanin ta. Sumi sumi dashi kai bakace zai iya kallon mace bama amma shine har ya iya birkita mata lissafi gaba d □□ ya yanzu.

Mi □ □ ewa yai ya sauka daga kan gadon ya koma kasa yana tsugunna wa, Hannuwanta ya riko dake tana bakin gadon.

□□ o na busar miki...□□

□□ an iya...□□

□□ oorulAyn! Bari na sanar miki HARSHEN ZUCIYA tah! Furanni na furta kalmomin yabo a kanki a dukkan lokacin da na shiga lambu mai d □□ uke da ruwa gami da korayen ciyayi da bishiyu masu d □□ uke da tsintsaye. Sukan rera baitukan yabo a gare ki, cikin harshen da zuciya ce kawai ke iya fahimtarsa. NoorulAyn ina kaunar ki sosai.. Akan kan ki na son so.. Soyayyar ta hob □□ asa ta zama kauna. DALAAL kasancewar ki mata agare ni, Ya zamo min alkhairin da ban taba zaton zan mallake

shi ba ko a mafarki, Kece mutum ta farko da a sanadiyyar ki ne na iya buda baki na na furtawa likita damuwa tah..!,

□□ in zamo min hasken idanu na...Kece gani na, Hasken da ke haskaka rayuwata! Farin cikin ki shine nawa, Bak □□ n cikin ki nawa ne. Kaunar da nake miki daga Allah ne. Ba zan iya rayuwa idan ba tare da ke ba NoorulAyn.. A mafarki da kuma a cikin soyayya babu abun da ba zai iya faruwa ba. Ina kaunar ki sosai hakan ya sa nake ji tamkar ba zan iya rayuwa idan ba tare da ke ba. Ba na fatan rasa ki a rayuwa ta, domin kuwa a dukkan lokacin da na rasa ki, na tabbatar da rayuwa ta za ta shiga garari. Ina miki kauna marar gauraye, Ke kadai ce cikin zucia tah, kuma ba zan taba canjawa a kan haka ba da yardar Allah.. Dan □□ ago ki kalle ni please, Hakan ne kadai zai tabbatar mun kin saurari kalamen zucia ta....!□□

Kalamen Hafezullah sunyi matuk □□ r tasiri ga DALAAL. Duk wata kofa ta jikin ta sai data amsa sakon harshen zuciar sa, Uwa uba zuciar ta, Ranta, Da ilahirin gangar jikin ta baki d □□ ya. Ta daga idanun ta cikin wani irin salo ta narke su akan sa. Caraf ya rike kallon nata ta hanyar zuba mata nasa idanun. Gashi kwayar idanun na Hafezullah manya dasu TubarkAllah! Irin sexy sleepy eyes dinnan ne dashi tamkar mai jin bacci. Zara zaran gashin idanun sa sun mike akan idanun. Nan suka saka shiga kallon kallo, Wanda ke bayyana adadin matsayin kowanne cikin zuciar dayan su.

Hafezullah ya katse kallon ta hanyar mi □□ ewa ya kamo hannayen ta baki d □□ ya. Ya tsayar da ita a gefen sa yana rankwafowa da kansa saitin idanun ta, Da tayi □□ asa dasu, Bil haqqi fa dalaal kunyar Hafezullah take ji.

□□ i kam bana cire kunyar nan ba ne...?Meyasa har yanzu ake yinta ne? Anya na gama cireta kuwa? Bari na duba...□□

Saurin ja tayi baya tana girgiza kai.

□□ llah! kaa cire.. Ka cire dagaske.□□

Takawa ya shiga yi, Tana baya da baya shi kuma yana cinmata daga gaba. A haka har suka kai bango Dalaal ta shige rike towel din gam. Hakan da take ba karamin dariya yake bawa Hafezullahi ba. Ya tokare duk hanyar da zata bi da dukkanin hannuwan sa, Ya sanyata a tsakiya. Ta shiga raba idanu tana kikkifta su.

□□ atsoraciya! Ni fa kawai tambayar ki zan yi... Ina dryer ta ke?□□

□□ at-tan- tana drawer.□□

□□ acce?!□□
Ya karasa tambayar ta yana janye gashin ta da ya zubo wajen idanun ta.

□□ accen...□□
Ta fadi tana nuna masa drawer din da yatsa.

Hannun ta ya rik □□, Suka karasa har wajen drawer din,

□□ annan?□□

□□ h..□□

Dakkowa yayi ya jona ta. Ya janyo teburin mudubi ya dora dalaal akai.

□□e zakayi?□□

□□usar miki zan. Karma ki wahalar mun da bakin ki wajen tambaya ta. Na iya!□□

□□ohm □□

Cikin □□warewa da wani irin salo ya shiga busar mata da gashin yana mikar mata da shi sosai. Idan ya yiyyi , Sai ya lakuto man kitson ta mai kamshi na yerwaincense& more ya shafa mata a gashin. Hakan da yake ba karamun tafiya yake da dalaal ba. Don dadi har bacci ne ya soma rinjayarta. Hafezullah ya koma kan gado ya zauna, Hade da kwanto da kan dalaal zuwa cinyar sa. Ya shiga busar mata da gashin yana mata oiling din sa. Sosai dalaal ta barar raje a cinyar Hafezullah tana bacci. Ya kashe dryer din yana mai gyara mata kwanciya yadda zataji dadin baccin.

Rankwafa wa yayi, Ya shiga kallon fuskar ta. Dadi ya sake mamaye shi. Wai shi Hafezullah shine ya samu dalaal a matsayin matar sa ta sunnah, Har sun kasance abu d□□ya? Wai yau shine ya busar da gashin dalaal? Gashin daya dade yana mararin mallakar mai shi. Ahankali ya saki tattausan murmushi,

□□lhamdulillah Yaa Rabb for the unlimited blessings! Alhamdulillah! Alhamdulillah! Allah kai ne abun godia.□□

Sun jima a haka, Tana ta baccinta ya janyo bargo ya lullubeta yanata murmushin farin ciki.

□⑩€□. □⑩€⑩€□. ._____. □⑩€□. □⑩€⑩€□.

Cikin bacci ta farka sakamakon shafe ilahirin jikin ta data ji anayi. Tana bude idanun ta. Taci karo dana Hafezullah ya zuba mata nasa tamkar zai hadiyeta.

□□in tashi..?□□

□□acci nayi?□□

□□una cikin drying da oiling kika fara bacci. Da alama nafi kowa iyawa. Domin don tsabar kwarewa ta, Har bakisan kinyi bacci ba.□□

□□an yamutsa fuska tayi tana cije lebenta, Hafezullah ya temaka mata ta tashi zaune. Shafa kanta tayi taji shi □□as a gyare yasha mai sai santsi da kamshi yake fitarwa.

□□agode..□□

□□a nayi me?□□

Nuna masa gashin tayi da hannun ta. Ya dan harareta da wasa yana hade rai kamar gaske.

□□aka ake godia??□□

□□oh ya ake yi?□□ Ta tambaye shi domin ta dauka wasu kalaman daban yake so.

Batai tsammani ba taji lallausan labban Hafezullah kan nata labban. Sumbatarta ya shiga yi cikin kwarewa da nuna tsantsar k□□una gareta. Sun dan dau lokaci a haka. Tana karbar sakon nasa, Kafin ya zare nasa yana maida numfashi itama haka.

□□ love you soo much.. Noorulayn.□□

Kasa ce masa komai tayi, Sai motsa hannuwan ta da ta shiga yi tana raba idanu. Ta mike da azama zata sauka daga gadon, Hafezullah ya riko ta yana murmushi,

□□ na zaki je?□□

□□ binci zan dora..□□

□□ i na soke yin abinci har na tsawon sati d□□ya, Mu fa sai yanzu muke cin amarcin mu.□□ Ya rada mata a kunnenta yana hura mata iska cikin kunnen.

□□ oh bara na sa kaya.□□

Sakin ta yayi ta mike, Doguwar riga ta dauka da undies ta shige cikin closet din gaba d□□ya dake babba ne. Shi dai Hafezullah murmushi kawai yake yi. Tana gama shiryawa ta fito.

□□ a hijabi fita zamu yi.□□

□□ ijabi kuma?□□

□□ h! Haka kawai baza□□ kallemin ke a kyauta ba.□□

Fitinar Hafezullah sai shi, Jilbab ta janyo kalar kayan ta saka. Ya sake kalleta daga sama har kasa yana yamutsa fuska,

□□ annan kara miki kyau ma yayi..Ba ki da niqab?□□

□□ ani da.□□

Matsawa yayi daf da ita, Ya sanya hannuwan sa biyu ya shiga gyaggyara mata fuskar jilbab din.

□□ a cika kishi..□□ Bakinta ya□□aro mata maganar da alama batamasan ta fada ba.

Hafezullah yayi murmushin gefen baki. Dimples dinsa suka lotsa,

□□ binda kakeso shi kake kishi akan sa hajjaju na.. Muje ko?□□

Ta ka□□a kai, Hannunta ya rike suka sauka har kasan, Ya bude motar da key, Sai daya fara zagayawa ya bude mata ta zauna, Ya gyara mata jilbab din daya zuraro tukun sannan ya rufe mata kofar, Ya koma wajen zamansa ya zauna ya tada motar da basmala da kuma adduar hawa abun hawa.

Suka hau kan titi. Sautin kira□□r maheer sai tashi yake, Hafezullah yana biye da karatun yana tukin sa ahankali. Hannunsa d□□ya kan sitiyari dayan kuma yana rike da hannun dalaal.

□□ na kikeson mu je? Gusto□□ko Bob□□?□□

□□ owanne...□□

□□ kay.□□

Kai tsaye ya wuce dasu wajen cin abinci na gustos. Wani waje reserved aka kai su. Da wakar masoya ta jaywillz (medicine) ke tashi ahankali.

□□ e zaki ci?□□
Ya tanbayeta bayan yaja mata kujera ta zauna.

Rik □□ menu din tayi tana kalla.

□□ ana cin abinci me nauyi da daddare.□□

Wani munafukin murmushi yayi yana kallon menu din,

□□ a kenan, Yanzu dole ki dinga buk □□ tar abinci me nauyi da daddare.□□ Ya fada yana maze fuska tamkar bashi yai maganar ba. Y □□ n miskilancin sun motsa.

Nunawa waiter din abunda za □□ kawo musu yayi. Ya karba ya tafi. Suka zauna zaman jigum jigum. Hafezullah ya daga wayar sa kamar yana dubawa, Ashe hotunan dalaal yaketa d □□ uka. Baiwar Allah bata sani ba. Tanata raba idanu. Waiter din ya kawo musu abincin.

□□ a appetizer nan. Mu fara da su.□□

Ta kad □□ kai tana ci. Tana korawa da lemo. Tana gama ci ya nuna mata plate din abinci kuma,

□□ i mana.. Ko sai na baki? Uhm?□□

□□□□ h zan ci.□□

□□ ohm □□

A nutse kowannen su yayi basmala suka fara cin abincin, Har suka kammala, Suka dora da dessert. Dalaal gaba d □□ ya ta koshi jin abincin take har wuya.

□□ an Allah ka barshi, na koshi wallahi.□□ Ta fada a marairaice ganin ya sake nuna wa waiter din wani abu a menu ya kawo musu.

Sallamar waiter din yayi, Ya danyi dariya yana girgiza kai,

□□ u tafi ko? Naga kina hamma.□□

Daga kai tayi alamun Eh. Ya mike hade da mika mata hannun sa. Ya zura nata cikin nasa suka nufi wajen mota. Ya bude mata tashiga, Sannan ya koma ya shiga ya tayar suka dau hanyar gidah.

□⑩€⑩€⑩€□<><><><><><><><><><><><>

*A hankali Hafezullah ya shiga bude idanun sa, Sakamakon kiran sallar asubahi daya ji anayi, Ya gama bude su tar kan dalaal data tukwikwiye shi, Da alama ta dauka bargon rufar ta ne. Zame ta ya shiga yi ahankali zai sauka ta sake janyo shi

tana lumshe idanu. Can ta bude su. Tayi saurin matsawa hade da cika masa rigar. Daria hakan yaba Hafezullah yayi sosai yana kallon dalaal,

□□ ajjaju kinga yadda kika yamutsa mun riga kuwa?□�

□□ ayi hak □□ ri.. Na d □□ uka pillow ne.□ Ta karasa tana nuna pillow dinta me siffar teddy bear.

Hafezullah ya danyi murmushi yana kallon kwayar idanun ta.

□□ arai kinsan ba shi bane, Kede kinason rab □□ r mijin ki ne, Zaki wani ce kindauka pillow ne.□

□□ llah dagaske.□

□□ oh Na ji, Atashi ayi sallah ko? Nima bara naje masallaci.□

Bandakin ya shige yayo tsarki hade da alwala, Ya sauya kayan baccin jikin sa zuwa jallabiya. Kai tsaye ya wuce masallaci. Yana fita ta dubi pillown nata tana hankadeshi gefe. Mikewa tayi ta shiga bandakin itama tayo tsarkin hade da alwala. Ta zura riga doguwa ta dora hijabi akai. Ta soma sallah. Ko bayan data idar ta jima tana azkhar hade da addu □□ i kafin ta mike ta ninke hijabin. Ta cire rigar ta mayar da kayan baccin. Can karshen gado ta kwanta bayan ta karkad □□ da addua, Tayi kwanciyarta ta hade da jan bargo ta rufe ilahirin jikin ta har kanta. Take bacci ya sace ta.

Cikin bacci ta soma jiyo tafiyar tsutsar da Hafezullah ke mata a jiki,

□□ eye haka..?□ Dalaal tafad □□ tacike da takaici, Domin bacci ne sosai take ji. Rabon ta da samun isasshen bacci tun lokacin data kai kanta wajen Hafezullah.

□□ akan ce ta kawo haka hajjaju..□
ya sake shigewa can jikinta, Ba yadda ta iya haka ta ky □□ le shi suka sake lulawa duniyar masoya. Wannan karon dalaal din ta sake tabbatarwa Hafezullahn na mata kauna ingatacciya. Domin bajintar da yake nuna mata, Ta zarcewa tunaninta □□ ima.

Basu farka ba sai da wayar Hafezullahi ta shiga kukan agaji, Wajen sau biyar. Dak □□ ar Hafezullah ya dauka yana girgiza kai,

□□ ssalamu Alaikum!□

□□ aalykm salam, Bro! Lapiar ka kuwa?□

□□ eya faru?□ Hafezullah ya amsa Habeebullah dake bambamin mita.

□□ au nawa na kira ka? Sau biyar, Matar ka sau 4 Honey pie na kiranta. Duk bakwa dauka, Yau asabar karfe 12 kuma Allah ya kyauta. Kar dai ka sururuta y □□ r mutane kaji na gaya maka..□

Hafezullah yayi shiru yana sauraren Habeebullah, Murmushi ya shiga yi yana girgiza kai,

□□ a gama?□

□□ h na gama □ Habeebullah ya amsa shi yana tsaki.

□□ oh ayi mana afuwa, Kasan rai dangin goro ne, Yana buk □□ tar hutu..□□

□□ an ta matse ku. Yauwa! Kuna da bak □□ yau. Zamuzo muku ziyara.□□ Kit ya katse kiran.

Hafezullah yayi dariya yana girgiza kai. Dalaal dake gefen sa ta shiga fadin,

□□ eya faru?□□

□□ ai sun kikkira bama dauka, Habeebullah ne da matar sa. Zasu zo anjima.□□

Ya karasa fada tare da gyara musu kwanciya. Ta ture hannun sa tana yaye bargon,

□□ o ai gwara mu tashi a fara shirin yi musu girki ko?□□

□□ u wa za □□ wa girkin? Mutanen da suka ci amarcin su bamu dame su ba, Sai yanzu da muke namu zasu daga mana hankali? Rabu dasu, Ai ya iya girki, Itama ta iya. Sai su girka mana.□□

Dalaal ta danyi daria tana girgiza kai,

□□ aba .. Baza □□ i haka ba.□□

□ □ ama wannan ba.. Ni fa banga ne ba Madam, Ya batun Sunana?bakya kiran sunana. Ba kuma kya gayamun wani me dad □□.□□

Ita dai shiru tayi tana lankwasa hannuwa.

□□ agana nake...□□ Ya rankwafo yana kallon dan karamin bakin ta.

□□ na zuwa.□□
Tai azamar mikewa hade da shigewa cikin bandaki, Wanka tayo sosai hade da yin brush. Ta shirya cikin wani lace mai launin peach. Ta saka dankunne da su sarka komai gold.

Hafezullah ya mike badan ya so ba. Ya shige cikin band □□ kin ya fello wanka shima. K □□ sa ya sauka ya shirya cikin riga da wando na shadda bai saka hula ba. Ya koma saman. Nan ya tarar harda gyara d □□ kin. Ta koma parlorn na saman shima tana tattare shi. Temaka mata yayi. Bayan sun gama suka karsa gyara kasan. Nan danan dalaal ta kukkunna turarukan wuta. Gidan gaba d □□ ya ya gauraye da k □□ mshin sandaliyya.

Indomie da kwai Hafezullah ya dafa da temakon dalaal dake gefe tana dariya , Suka koma parlor suna ci. Suka kammala Hafezullah ya kai kitchen ya dan dauraye daga tsaye ya kife yadda yaga tana yi. Ya koma ya ganta ta mike tana duba waya.

□□ enene?□□

□□ abeelah na kira nace naga missed call d □□ nta.□□

□□ kay...□□

□□ amar da me dame kake ganin za □□ musu? Ko ka tambayar mana Habeeb din. Kar nayi abunda basu so, Ko suna da allergens dinsa.□□

□□i nace ba ke ba girki sai kinyi sati d □□ya, Ki rabu dasu.□�

□□ak □□n ka an..□�

□□arma ki karasa NoorulAyn. Akwai komai a kitchen su dafa abunda suke so ko ai ordering na waje.□ Ya karasa yana sanya dan yatsansa d □□ya kan bakinta data bude zatayi magana.

Ba yadda ta iya, Ta mike tayi kwanciyar ta, Hafezullah ya gyara mata kwanciyar ta hanyar dora kanta kan cinyar sa, Yana shafa gashin ta. Suna kallon shirin indian film na □□ hate love story.□ Ba jimawa sosai su Habeebullah suka iso.

Sunyi matukar kyau shi da matar sa nabeelah , Ta shirya cikin abaya baka. Shi kuma Habeebullah yasa Manyan kaya. Door bell suka danna. Hafezullahi ya hana dalaal tashi, Ya isa ya bude musu yana murmushi. Habeebullah ya zabga masa harara. Suka wuce ciki baki d □□ya. Hannun Habeebullah da ledoji har biyu.....

#Tawan ta gaban goshin uncle Abdul, Gaskia Hafezullah din naki sai a slow □□□□ Man kansa rawa yake □□...!!!

*_□ AL-□IBLA_*□□
Na Safiyya Huguma

*_□ MABU□IN ZUCIYA_*□□
Hafsat Rano

*_□ DALAAL_*□□
Na Miss xoxo

*_□ UBAYD MALEEK_*□□
Na Mamu gee

*_□ MAKAUNIYAR □ADDARA_*□□
Na Bilyn Abdull

Lalai daga ji babu tambaya bana ma ZAFAFAN ku da turirinsu suke tafe. Dan dagani kasan za'a ragargaza cakwakiya, soyayya. Tare da nisha □i □□□□□□□□□□□□□□□□□.

Gasu duka akan farashi mai rahusar gaske.

Kamar haka □□□□□□□□

□aya___300
Biyu____400
Uku_____450
Hu□u____500
Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki □□□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban ta whatsapp shedan biyanku(evidence of payment/Account name)□□□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU □□□□

□ 0903 □ 234 □ 5899

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
TEAM----ZAFAFA BIYAR □□□□□□□□
10/22/21, 10:26 PM - Buhainat: _DALAAL □□□□□□_
(A new world/Destiny □□ love)

_56_

_*ZAFAFA 2021! NEXT LEVEL_*
_*ZAFAFA 2021! NEXT LEVEL_*
_*ZAFAFA 2021! NEXT LEVEL_*
_□ □ □ □ □ □ □ □

□ □ □ □ □ □ □□□□□□□□□ □□

_*INA MASOYA MAKARANTA ZAFAFA BIYAR MASU SON SAI ZAFAFA SUNYI NISA ZASU SAYA? TOH KU MATSO, DOMIN ZAFAFAN LITTATTAFAN NAKU SUNYI NISA, DAI DAI DAD'IN KARATU_*

_*YAN BIYAR DIN NAKU KAMAR KO YAUSHE SUNA TSAKA DA RUBUTA DADAD'AN LITTATTAFAN SU MASU TAFIYA A TSARE, CIKE DA FADAKARWA, NISHADANTARWA DA KE TAFE DA RANTSATTSIYAR KAUNA MARAR GAURAYE.._*

_*SHIN YAR KUWA KINA DA LABARIN ZAFAFAN WANNAN KARON MA KUDIN SA NA PAGES NA YADDA YAKE KAMAR NA BAYA? DUKKA LITTAFAN BIYAR DIN BABU NA YARWA, KOWANNE DA KALAR DADIN SA_*

□ □ □ □ □ □ □ □ □ □ □ *1*

_*DAGA TASKAR SAFIYYAH HUGUMA: WANNAN KARON TA ZO DA WANI SABON SALON LITTAFINTA MAI SUNA : *ALKIBLA* *(THE BATTLE OF LOVE) WANDA KE KUNSHE DA FADAKARWAR RAYUWAR SAMARI DA YAMMATAN YANZU, AKWAI RANTSATTSIYAR KAUNA DA KE WATANGARIRI DA ZUKATAN MUTANE BIYU: ZAHRA DA ALIYUU □□□□□_*

□ □ □ □ □ □ □ □ □ *2*

_*SAI DAGA ALKALAMIN HAFSAT RANO, WANNAN LEVEL DIN TAZO DA NATA KALAR RUBUTUN MAI TAKEN: MABUDIN ZUCIYA! (LOVE/HATRED) MABUDIN ZUCIYA NA TAFE DA FADAKARWA AKAN HAKKIN GASKIYA DA AKASINTA, CAKWAKIYA CE DAUKE DA LITTAFIN WANDA WARWARAR SA NA GA ZUKATA BIYU, RAFEEQ DA AYSHA □□□□_*

□ □ □ □ □ □ □ □ □ *3*

_*DAGA ALKALAMIN MAMUH GEE! WANNAN TAFIYAR TAZO DA NATA SALON MAI SUNA: UBAYD MALEEK(ROYALTY/LOVE) WANNAN KARON KASAR ETHIOPIA TA SHALLARA TA DAKKO AL'ADUN SU MAI CIKE SA FADAKRWA, MUSANMAN AKAN ZAMANTAKEWAR AURE, YA ZATA KAYA NE GA SOYAYYAH GA SARAUTA? WANNAN AMSAR NA WAJEN UBAYD DA NURU!□□□□_*

□ □ □ □ □ □ □ □ □□ *4*

_*SAI DAGA ALKALAMIN NANA HAFSATU (MISS XOXO) WANNAN KARON TAZO DA NATA TAKEN LITTAFIN MAI SUNA: DALAAL! (A NEW WORLD/DESTINY's LOVE) LITTAFIN NA DAUKE DA FADAKARWA MUSANMAN DANGANA DA HAKURI, YA ZATA KAYA NE DA SOYAYYAR ZUKATU UKU, HABEEBULLAH TAGWAN (TWIN) HAFEZULLAH, GEFE DAYA GA DALAAL DA AKEYI AKANTA?SHIN WA ZAI YARDA YA BARWA DAN UWAN SA?□□□□_*

□ □ □ □ □ □ □ □ *5*

*SAI DAGA KARSHE, BILYN ABDULL! NA TAFE DA NATA SALON MAI SUNA: MAKAUNIYAR KADDARA!!! (BLIND LOVE) LITTAFI NE DAKE DAUKE DA FADAKARWA MUSANMAN KAN KADDARA DA KE FADAWA DAN ADAM, NATA SALON KADDARAR MAKAUNIYA CE, GEFE DAYA LITTAFIN NA DAUKE DA SALON RANTSATSSIYAR KAUNA AKAN ZINNEERAH... DA BATALIYAR MASOYANTA, MUSANMAN MODIBBO!□□□□_*

_*DUKA WADANNAN LITTATTAFAI NA ZAFAFA NE DA AKEYI A HALIN YANZU, KUMA KUDINSU NAIRA 700 NE PAGES. DUKA BIYAR DIN. KU GARZAYO KU MALLAKI NAKU TUN DA TURURUN SU, LITTATTAFAN ZAFAFA SUNYI FICE A YANAR GIZO, KU ZO A DAMA DAKU A WANNAN TAFIYAR TA NEXT LEVEL, MASU SANA'OIN HANNU MA MUNA TALLATAWA AKAN FARASHI MAI RAHUSA_*

_*DOMIN MALLAKAR NAKU, KU TUNTUBE MU TA KARSHEN SHAFIN KASA □□□□_*

*****Karasawa ciki suka yi baki dayan su. Dalaal ta lullube jikin ta cikin wadataccen mayafi peach color, Suka rungume juna da Nabeelah. Kafin su zazzauna baki dayan su.

□□ na wuni Ya Habeeb?□ Dalaal ta gayshe da Habeebullah cikeda girmamawa.

□□ apia kalau siss. Ya gidah da al □□ mura?□

□□ lhamdulillah.□

□□ asha Allah!□

Nan Hafezullah da Nabeelah ma suka gaysa, Kafin shi da Habeebullah din su tafa suna gaysawa.

□□ a banga kuloli ba?□ Habeeb ya fad □□ yana jefawa Hafez Kallo.

Nabeelah ta danyi dariya tana kallon Habeeb din

□□aba, Sugar pie..!Munci abinci fa, Karka tashe su a tsaye.□□

Hafezullah yayi dariya sosai. Kafin ya mike ya shiga kitchen ya kawo musu lemuka da ruwa da snacks.

□□i sun san da zuwanmu tunda na kira wannan dan renin hankalin da sai da yaga dama tukun ya dauka.□□

Hafezullah ya kaiwa Nabeelah nata har gabanta, Kafin ya mik□□wa Habeeb yana dariya,

□□ace zata dora na hanata, Tace na ma kira ka na tambayi abincin da kukeso, Kar tayi wanda bakwaso ko kunada allergens dinsa.□□

□□oh akan wane dalili zaka hanata aikin lada? □□ Habeebullah ya tambayi Hafezullah.

Su dai Nabeelah da Dalaal sai dariya suke.

□□ata jin dadi ne, Kuma naga kai da Nabeelan kwararru ne a fannin girki, Ka manta sanda naje kana zayyano mun abubuwan da kake dafawa? Har ma naci pepper soup din da kayi.□□

Habeebullah ya zabga masa harara yana girgiza kai,

□□aka ha□□uba gaskia, Au duk tunanin ka ni da honey pie ne zamu shiga kitchen mu girka muku abinci kai da matar ta ka?□□

Hafezullah yayi dariya sosai kafin yace dashi,

□□o ma kai da lemon pie ne. Ai kune manyan mu. Muna bin sahun ku ne.□□

Habeebullah yaja dogon tsaki yana hararar Hafezullah da wasa kafin yayi dariya kawai ya dauke kai,

□□is munzo cin abincin amaryar mu kuma marowacin angon ki ashe ya hana?□□

Dalaal tadan yi murmushi tana fadin,

□□i kuwa dai ba yadda ban dashi ba.□□

Nabeelah ta katse maganar ta hanyar cewa.

□□u dai munzo sake tausasar ran kanwar mu ne, Abubuwan da suka faru a baya a te..□□

Dalaal tayi saurin katse ta,

□□aba sis, Haba! Allah ya kiyaye..! Wallahi na mance ma, Ai an wuce wajen. Dan Allah kada ku sake maido ta. Da Ya Habeeb din da Ke dear sis, Da shi dik na yafe muku.. Nima ku yafemun kan abubuwan da na muku da ba kuji dad□□ba.□□

□□aye shi din?□□ Hafezullah ya taso ya koma kusa da ita yana cusa idanun sa kan nata.

□□ace waye shi din?□□

□□abun shigar soyayyah. Dalla malam koma inda kake zaune, Ko kunyar mu bakaji, Ina babban wanka ga matata awajen kana wani.. Dalla matsa.□□

□□asu tafi ne, Zan gamu da ke...□□ Hafezullah ya radawa Dalaal a kunne yana dan cizan kunnen Kadan. Wanda yasa ta saki yar kara.

Komawa yayi gefen Habeeb ya zauna,

□□aye babban wan nawa?□□

□□i mana.. Kanada wani bayan ni ne?□□

□□i baka girme mini ba, Kaji ka wani zance.□□

□□ana d□□ya aka haife mu?□□

□□□□h..□□

□□oh ko da second d□□ya ne na girme maka ballantana kwana da wuni cir, Dalla matsa. Sis! Kamar yadda honey pie tafada dan Allah ayi mana gafara, Ni me lefi ne, Nayi kuskure ..□□

□□llah Ya Habeeb ya wuce, Karkaji komai, Har gaban abadan.□□

□□alle na yadda ya wuce. Ga suna nama an □□aramun da Yaya. Godia nake k□□nwata! Allah ya miki albarka, Ya kara muku zaman lapia da mu baki d□□ya. K□□fa a bude take duk abunda dan □□anina zai miki na rashin kyautatawa ki sanarmun zai ji ajikin sa.□□

□□oh Babban Yaya.□□

Haka suka cigaba da wasa da dariyarsu abun su. Habeebullah ya mike yana nannade hannuwan rigar sa,

□□ashi muje muyi girkin da kai.. Honey pie ku cigaba da hirar ku.□□

Hafezullah ya mike yabi bayan sa suka shiga kitchen. Ya nunnuwa Habeebullah kayan girkin da komai,

□□ara dauraye tukwanan.□□

□□ai kuma fa?□□ Hafez ya tambayi Habeeb dake bashi order.

□□i ba wanka ba ne? Dauraye su saboda ba□□san meye suka shiga ciki ba, Then sai mu dafa farar shinkafa da onion sauce. Sai mu gasa kazar akan abun gashin can.□□

□□i fa ban iya girki ba Bro.□□

□□hap zaka koya yau. Da rarrafe yaro kan iya tafiya.□□

Haka dai suka gama musun su. Tukun sannan suka shiga girkin, Basubar kitchen d□□nnan ba sai da suka kammala komai. Suka koma parlor. Abincin kuwa babu lefi yayi dadi. Su Dalaal sai santi suke yi. Bayan sun gama ci. Su ka fita sallah a

masallaci. Suka dawo gwanin sha □□ wa. Nan Habeebullah yabar Nabeelah kan su cigaba da hirar su zai dawo ya dauketa da daddare.

□□ inti d □□ ya!□ Hafezullah yace da Dalaal yana kafe ta da idanu.

Suka shiga d □□ ki, Habeebullah ya matsa kusa da Nabeelah shima yana neman magana.

□□ amu je gidah ne. Mu dasu Baba zamu karba ku □□ i da kayan lefen su Ayaah da yan biyun Mama ikhlima Nasrean da Aliya.□

□□ oh sai kun dawo Allah ya dawo mana daku lapia.□

□□ amin, Shikenan?□ Ya tambayeta yana kanne mata idanu.

Gudun fitinar sa tadan yi □□ age kadan ta sumbaci gefen kumatun sa. Hafezullah yayi dariya yana lakuce nata kumatun da hannun sa,

□□□□ r gari kenan, Har kin soma d □□ ukar darasin ko, Idan na dawo anjima zamu dora akan wani.□

Ita dai bata kuka shi ba. Suka fito hannun sa sarqe cikin na juna. Habeebullah ya mike daga jikin Nabeelah shima. Suka fice bayan dalaal da Nabeelah sun had □□ baki wajen musu addu □□ r zuwa da dawowa lapia..

Suka cigaba da hirar su gwanin sha □□ wa, Suna kuma bawa juna shawarwari. Sai dare tukun sannan su Habeeb suka dawo da abinci a kuloli sun taho dasu daga gidah. Suka zauna gaba d □□ ya sukaci sunata zumunci. Da zasu tafi Dalaal ta cikawa Nabeelah leda da kayan turaruwa na fesawa dana gidah hade da spices na girki.

□⑩€⑩€□. □⑩€⑩€□. □⑩€⑩€□.

Haka rayuwar su tacigaba da tafiya cikin lumana, Kwanciyar hankula da kuma kaunar juna. Safiya ta zama rana, Rana ta zama yammaci, Yammaci ya koma dare. Lokuta nata ja, Sosai shak □□ wa hade da kulawa ta wanzu a tsakanin su. Sai hamdala kawai.

**Tana tsaye gaban mudubi ta zuba kyau cikin wata tsadaddiyar shiga ta alfarma. Atamfa ce akayi mata d □□ nkin da ya mata □□ as a jiki. Irin 3 quarter riga dinnan mai zuwa gwiwa, Sai skirt straight, Ya amshi kyakkyawar kirarta. Tayi kyau ba kadan ba.. Tana ta kiciniyar saqala chain din sark □□ Hafezullah ya shiga dakin, Shima ya zabga ado cikin riga da wando na shadda. Ya murza hula. Ba kadan ba shima yayi kyau.

□□ oorulAyn □

□□ hm! ! NoorulHayat! Ka dawo...?□

□□ a dawo yanzu....□ Ya karasa fada yana saqala hannuwan sa a ruwan cikinta. Ya dora kansa kan kafadarta yana sumbatar gefen wuyan ta. Suna kallon kansu ta cikin mudubi.

Ahankali tamkar muryar rad □□ yace,

□□inyi kyau... Mi Amor (My love)□□

□□agode Mi Alma...(My soul)□□
Ta fada tana mai dago hannunta d□□ya ta shafa habar sa.

Karbar sarkar yayi, Ya zura mata a wuyan nata. Ya shiga shafa kan sarkar tata yana lumshe idanu. Hannunsa na kokarin shiga saman rigarta, DALAAL ta goce tana dariya.

□□hm! Uhm na □□i wayon..Lada ya kare. Muje ko?□□

□□ai wani zumud□□kike, Allah sai na hana ki.□□ Ya karasa yana kwafa.

Dalaal ta riko hannun sa tana turo baki gaba, Hade da tattare fuskarta tayi kalar tausayi.

□□ls...Kaji..My baby □□

Dariya yayi. Kafin ya riko hannunta d□□ya, Dayan kuma ya d□□uki jakarta suka sauka kasa. Kai tsaye suka wuce parking space.. Ya bude mata gaba ta shiga, Shi kuma ya koma mazaunin driver ya zauna. Ledar dake hannunta ta mayar kujerar baya. Hafezullah ya tada motar da bismillah hade da adduar hawa abun hawa. Balele ya bude musu gate suka fita.

□□na ma kika ce?□□

□□ai kuntau..Ka sani ko?□□

□□a tambayi kwatancen. Ba damuwa ga map nan zamu da yardar Allah.□□

Tafiya suke akan titi. Garin yayi dadi. Ya kuma yi luf, Ko□□na yayi shar. Bishiyu sun sake turuwa. Ahankali Hafezullah ke tafiya. Ga ruwa da ake yayyafa. Wata wa□□ar masoya ce ke tashi ahankali ta calum scott mai taken: You are the reason. Hannun Hafezullah d□□ya yana driving dashi d□□ya kuma yana saqale dana Dalaal.

□□here goes my heart beating
'Cause you are the reason
I'm losing my sleep
Please come back now
And there goes my mind racing
And you are the reason
That I'm still breathing
I'm hopeless now
I'd climb every mountain
And swim every ocean
Just to be with you
And fix what I've broken
Oh, 'cause I need you to see
That you are the reason
There goes my hands shaking
And you are the reason
My heart keeps bleeding
I need you now...□□

Ahankali shi da ita suke bin wak□□r, Gwanin sha□□wa. Komai nasu a bun burgewa ne. Kuma yawanci dik abunda d□□ya yakeso d□□ya ma yana so. Hafezullah ya gangara bakin titi ya faka motar yana murmushi.

□□eya faru...?□

□□can□□go anywhere, Let□□fuel up.□

□□hat?!!!! Amma NoorulHayat kace kasha mai fa...Dama baka zuba man a motan ba?□

Wani murmushin ya sake yi, Ya ja kasan leben sa yana danna wani madanni. Kujerar Dalaal tayi baya. Zare seatbelt din jikin sa yayi. Ya matsa kusa da ita, Batayi aune ba taji ya dora labban sa kan nata. Wata irin sumba ya shiga yi mata mai ratsa jiki. Dalaal tayi luf tana karbar sak□□n sa. Domin Hafezullah ya riga ya kere tunaninta a fagen soyayya. Soyayyah yake nuna mata ta bajinta yar asali. Sai daya sumbaceta sosai sannan ya daga bakin sa yana murmushi.

□□□□full now, Let□□go...□
Ya fada yana dariya.

Lakuce masa kumatun tayi tana girgiza kai. Ta mike tana kallon kanta a mudubi. Jambaki ta zaro a jakarta ta sake shafawa,

□□inyi guzuri kenan.□

□□hap! Ai nasan hali.... NoorulHayat, I won□□ever leave you, Not for a second. Till death do us apart Insha Allah.!□

□□o na□□ara wani ne? Dama bai ishe ni ba... NoorulAyn! If i knw what love is, Its because of you. Never leave me alone please. I would be an empty flame without you in my life. I love it when you say. ' I won't ever leave you, not for a second..□

□□an Allah kayi hak□□ri mu dawo... I love you sooo much...□

Murmushi yayi. Ya sake matsawa ya sumbaci goshin ta, Da kumatunta kafin ya tada motar suka cigaba da tafiya. Sannu ahankali har suka karasa unguwar kuntau. Wani layi mai kyau dashi yasha gate. Dalaal ta dauki wayar ta tana duba kwatancen da Hissah ta turo mata. Har kofar gidan suka karasa ba nisa.

□□lhamdulillah mun zo...□

□□mma zaka shiga ko?□

Yai saurin girgiza kai yana murmushi,

□□i kinsan bazan iya ba.□

□□e tsoron mutane kawai..□

□□aji din. Na baki minti 10 ki fito..□

□□aba NoorulHayat.. Na dauka ma sai can dare tukun.□

Wata uwar harara ya watsa mata yana kauda kansa, Kafin yayi murmushi itama ta yi.

□□ an dawo da yamma na dauke ki Insha Allah.□□

□□ akan ma nagode.. Sai ka dawo NoorulHayat, Allah ya tsare mun kai.□□

□□ amin NoorulAyn, Ki kular mun da kan ki...□□

□□ nsha Allah... Bye.. Luv Ya □□
Ta karasa tana hura masa kiss.

Har ta shiga gate din tana daga masa hannu, Shima yana daga mata. Yaja motar ya tafi. Ita kuma ta shiga gidan. Gidah ne sama da kasa na bene. Hissan a kasa take. Kishiyar kuma a sama. DALAAL na sallama, Hissa tafito da sauri tana rungumeta,

□□ ayyo Allah dadi. Sannu da zuwa Sis! Shigo shigo, Lale maraba.□□

Cikin wani babban parlor suka shiga. Mai dauke da kujeru da kayan kallo. Kasa zama Hissah tayi. Ta kakkawowa dalaal ruwa da lemo.

□□ aki cemun yau zaki zo ba sis. Ai dana hada miki kayan dadi na musanman. Yanzu ma bata baci ba, Bara na shiga kitchen.□□

□□□□ h wallah..Karki wahalar da kan ki, Nasan zaki hidimar shiysa ma naki gaya miki. Wallahi a koshe nake.□□

□□ ai sissy! Yanzu ba zaki ci komi a gidah na ba?□□

□□ oh zanci wainar fulawa dinnan, Kin ma iya girki kuwa Hissah?□□

Hissah tayi dariya tana girgiza kai,

□□ anin da kika yimun sissy, Ai Aunty kafin auren nan sai data sa ni a catering school kuma sisters dinta ma sun kara kokkoya mun na gargajiya.□□

□□ h! Masha Allah! Haka akeso.□□

□□ ara na kunna miki kallo.. Kafin na soyo mki □□

Ta kunna mata kallo. Dalaal ta mayar da hankalin ta kan kallon. Sai ga wasu yara sun shiga su 4, Hancin su dagaje dagaje da majina. Suka dane kan kujerun Hissah da kafafuwan su da sukayi furu furu da □□ asa.

□□ unty! Aunty...□□

Suka shiga kwallawa Hissah kira, Dalaal ta zubawa sauratar Allah idanu. Gashi sun zuba mata idanu suna bin ta da kallo kamar zasu hadiyeta.

Hissah ta leka da kanta ta kitchen din tana musu magana,

□□ biru, Ya akai?□□

Basuyi magana ba suka fita da gudu. Su hudu duk maza kusan kansu d □□ ya ma. Biyu manya biyu k □□ nana,Kana kallon su kasan yayye ne da kanne. Tana gama soya

wainar ta zuba a karamin food flask. Ta dora akan babban tray da plate da yaji da kuma yankakkun kananun tumatir da albasa. Sai tashin kamshin tafarnuwa yajin yake.

□□a shi sis.□□

□□ai har an gama? Nagode sosai, Na tashe ki a tsaye.□□

□□abu komai wallahi. Ina yini sis, Ya mai gidan naki Harees?□□

□□arees kuma? Ko dai Hafez? Yananan kalau. Alhamdulillah! Yana gayshe ku.□□

□□u haka fa. Alhamdulillah mungode.□□

□□annan yaran waye da suke leko mu?□□ Ta tambaya tana nuna yaran dazu da suka shek□□a guje.

Hissah ta sauke zuciya tana murza hannayenta cike da damuwa tace.

